Copied By
HAYATU BABA ZUBAIRU
(admin
Hayat hausa novels
Hausa novels and fashion
Cool novel, makeup and kitchen1️⃣
AND
Cool novel, makeup and kitchen2️⃣)

WHATSAPP NO:
+2347039625239
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: [3/6, 11:13 AM] Fdaus Sodangi: *KAINE SANADI!* 1️⃣

*WRITTEN BY*:

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY:*
*KHALISAT HAYDAR*

*EDITTED BY*
*SANAH S ISMA'IL MATAZU*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

_Bismillahirrahmanirrahim_

_Godiya ga ubangijin mu Allah daya bani ikon fara rubutun nan lafiya, ina rokon Allah yasa inkare lafiya batare dawata matsala ba Ameen, wannan labarin kirkirarrene banyi shi dan cin zarafin wani ba kowata, idan yayi shige da labarin rayuwar ki ko naka ina niman afuwa hasashe ne dakuma aikin alkalami wanda yafi na takobi.

D'akin d'aukar karatun a cike yake taf babu masaka tsinke, duk inda ka waiga babu alamar zaka iya samun wajan zama domin kuwa d'alibai ne tako ina, duka-duka k'arfe takwas ne na safiya amman kuwani d'alibi ya halarci lecture d'in kasan cewar sam mallamin babu wasa bare d'aga k'afa a tattare dashi, gashi yau d'in nan suna saka ran zaimasu test, duk kuwa da bawai ya fad'a cewa zaiyin bane, amman da dukkan alamu suna saka ran zaiyi d'in, dan shi haka yake badai yace zaiyi abu ba, saidai ya shammace ku yayi d'in.
Hayaniyar d'aliban ne yacika d'akin karatun, wasu na hira, wasu na karatu wasu na bacci, yayinda wasu keta faman cece kuce.

Lokaci d'aya d'akin ya d'auki shuru, tsit kakeji tamkar ba sune keta hayaniyar nan ba, masu bacci tuni sun tashi, kowa ya kama kansa yashiga taitayin sa.

Matashin malamin ne yashigo, wanda k'amshin turaransa ya sanar wa d'aliban nasa ya iso.

K'yakk'yawan matashi ne wanda shekarun sa na haihuwa bazasu haura 30 ba, wankan tarwad'a ne dogo sosai ga fad'i, yanada manyan idanuwa had'e da yalwataccan gashin gira dana ido, ga wani had'add'an sajensa wanda yak'ara fitowa da k'yawun da Allah yai masa, hancin sa dogo mai k'yawun gaske.
Sanye yake cikin k'ananan kaya, bak'in wandon Jeans ne had'e da wata jar riga mai azababben k'yau, rigar ta d'an matse shi kad'an saita k'ara fiddo shi, k'afar sa sanye cikin wasu had'add'un takalma na maza, dagani kasan masu tsata ne, wani dank'areran agogo ne d'aure a tsintsiyar hannun sa mai kalan bak'i sai wani shek'i yakeyi tamkar daimon.

*ALIYU RASHEED GANDUJE* kenan, matashin malamin dake lokacin sa a jami'ar ta *CATHOLIC UNIVERSITY OF AMERICA*, cikin takunsa ta k'asaita ya isa gaban d'akin karatun, inda ya k'arasa sama inda ya dace ya tsaya d'in, tsawon minti uku ya d'auka a tsaye yana k'arewa d'aliban nasa kallo d'aya bayan d'aya, idanuwan sa suka fad'a gun zamanta inda yaga wayam batazo ba, illa k'awar tata mai suna, *KHADIJA MUHAMMAD DALA* murmushi yasaki wanda ya tsaya a fatar bakin sa, gaba d'aya d'aliban nasa sunyi mamakin ganin murmushin nasa dan sabon abu ne agare su, wannan ne yasa kowa yak'ara shiga taitayin sa, dan acewar su murmushin mugunta ne wannan *ALIYU RASHEED GANDUJE* yayi, cikin k'warewa yashiga koyar dasu daki-daki, gaba d'aya hankulan su nakan sa ko motsi mai k'arfi babu maiyi acikin su, tsawon minti talatin yanai masu darasin.

K'was!! K'was!! K'was!! K'arar takalmin nata ke bada sauti, kasancewar wajan yayi shuru shiyasa k'arar ya karad'e ko ina, shi kansa *ALIYU RASHEED GANDUJE* cak ya tsaya daga bayanin sa yana kallon ikon Allah, shidai yasan cewa babu d'alibin daya isa yashigo mashi aji bayan shi d'in yashigo, dan wannan rainin wayau ne babba acewar sa.

Hankalin ta k'wance taci gaba da takunta tana k'arasowa cikin d'akin karatun, tafiya take cikin yanga da tak'ama, kallo d'aya zakai mata ka tabbatar dacewar babbar yarinya ce kuma d'iyar wani babban mai mulki da sarauta, zaka gane hakan ne ta yanayin shigar ta dakuma yanayin yanda take tafiyar tamkar bazata taka k'asar ba, k'yakk'yawa ce ajin farko, tsayawa in k'watanta maku k'yawunta k'arin bata lokaci ne gara kawai inbarku ku k'watan tota da kanku masu karatu,
*AMATULLAHI AHMAD FAGE* kenan matashiyar budurwar da babu kamar ta acikin jami'ar, wajan k'yau da tak'ama dakuma nuna isar cewar ita d'in fa d'iyar shugaban k'asa ce, wohoho.....

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*
[3/6, 2:36 PM] Fdaus Sodangi: *KAINE SANADI*2️⃣

*WRITTEN BY*:

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY:*
*KHALISAT HAYDAR*

*EDITTED BY:*
*SANAH S ISMA'IL MATAZU*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

_Yawan comments d'inku shi zai k'ara k'arfafa min gwuiwa, insan Ibrn nada masoya indage wajan yin typing dasauri_

Tafiya take ko ina na jikin ta na k'adawa duk da doguwar riga ce ajikin ta amman saboda kayan datake d'auke dashi wanda Allah ya halicce ta dashi, dole ne jikin nata ya kad'a abin gwanin ban Sha'awa, gaba d'aya kallo yakoma kanta, itakuwa tafiyar ta take hankali k'wance tamkar ita d'aya ce a duka filin d'akin haka take ji, tana k'ok'arin zama bisa kujerar daya zame tamkar dan su aka yishi ita da k'awar tata wacce duk sanda tariga ta shigowa sai ta aje mata gu, kai koma duka basu zo dawuri ba babu mai hurumin zama a kujerar dan kuwa kowa yasan wacece *Amatullahi Ahmad Fage* da k'awar ta *Khadija Muhammad Dala*, wani wawan tsawa yadaka mata, cikin harshan turanci yasoma magana, "You are very stupid wacece ke dazaki shugo min aji yanzu har kike k'ok'arin zama dan bakida kunya bayan kin d'aukewa kowa hankali daga sauraron abu mai mahimman ci!"
"will you get out before I slap your dirty face!"

Cak taja ta tsaya tana masa wani k'ask'antaccan kallo, kafin taja wani dogon tsaki da k'wafa tamkar harshan ta zai fita, ta doka masa wata uwar harara da manyan idanuwan ta tamkar zasu fad'o k'asa, tafice a d'akin karatun cikin wannan tafiyar tata mai d'aukar hankali, harta bace daga cikin d'akin baibar kallon inda tabi ba, zuciyar sa tamkar ta fasa k'irjin sa tafito, lallai yazama dole yayi maganin yarinyar nan, aduk fad'in jami'ar nan ita k'adai ce ke taka shi son ranta, but lokaci yayi daya kamata yanuna mata iya karta yanuna mata ita d'in fa ba kowa bace!,

Hankalinsa ya maida kan abinda yakeyi, gaba d'aya ajin kowa yasha jinin jikin sa dangane da abinda yafaru yanzu,

Awa d'aya ya bata yana koyar dasu kafin yabasu test, hankalin Khadija ne yayi bala'in tashi dan ganin k'awar tata bata nan yabada test d'in, takuma san da gangan yayi hakan saboda wannan shine test d'in shi na k'arshe yace, har nanata masu yayi duk wanda yarasa wannan test d'in to kada yasaka ran zaici jarabawar sa, nan danan idanuwan Khadija suka kad'a sukai jawur dan bacin rai, "wai shi wannan d'an talakawan me yake tak'ama dashi ne?" waye shi dayake taka _Amatullahi_ haka? Gaskiya dole suyi maganin gayan nan dan isar shi tayi yawa yanaso yawuce gona da iri.

Minti ashirin kacal sukayi yasa a k'arbar masa,  ana gama had'awa ya fice abinsa,  zaune ya iske ta akan wani had'add'an Capet mai kama da jikin damisa sai d'aukar ido yake, guys d'in ta zagaye da ita kowanne ya d'od'e ido cikin bakin tabarau kallo d'aya zakai masu ka tabbatar basuda mutunci zasu iya aikata komi akan aikin su.

Manyan idanuwan ta ta watsa akan sa tare daja masa tsaki, kallo d'aya yaimata ya d'auke kansa daga barin kallon ta, yawuce abinsa, d'aya daga cikin guy's d'in nata yayi k'ok'arin binsa saboda tsakin dayayi, ta dakatar dashi da fad'in "barshi ba Yanzu ba akwai sauran lokaci!".

D'aliban ne suka suma fitowa daga d'akin karatun kowanne na surutu akan test d'in da _Aliyu Rasheed Ganduje_ yayi.

Khadija ce tafito rannan nata a had'e ta zauna kusa da k'awar tata tana labar tamata abinfa Aliyu Ganduje yayi, tsaki Amatullah tayi tace "karki damu k'awata indai kud'i suna aiki a duniya zan saye Aliyu Ganduje dashi da y'an gidansu gaba d'aya,  dan haka ki barni dashi shi ai k'aramin d'an iska ne!".
Murmushi Khadija tayi ta bata hannu suka kashe, tace har naji sanyi a zuciya ta wallahi gayen baida mutunci, hira suka ci gaba dayi abinsu cikin k'wanciyar hankali harsanda wani malamin yashiga ajin kafin suka mik'e suka shiga suma.

Tsawon wani lokaci malamin nayi masu darasi kafin yafara watso masu tambayoyi,  tsit ajin yayi dan kuwa tambayar tad'an yimasu wuya, tsawon minti uku babu mai alamar mik'ewa, tambayar malamin yak'ara nanatawa cikin bacin rai amman tsit kake ji, ajin yad'auki shuru dayawa, can wani had'add'an gaye daga baya ya mik'e cikin turancin sa mai dad'in saurare yasoma watso amsar tambayoyin, *MUHAMMAD HUSSAIN D'ANBATTA*
kenan Yaro mai tarin baseera da hazak'a.

Wani dogon tsaki Amatullah taja tare da fad'in banza d'an scholarship kawai!, mutum sai iyayin tsiya kowa yayi shuru amman shi yawani mik'e da banzan turancin sa saikace d'an koyo.........

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*
[3/6, 5:14 PM] Fdaus Sodangi: *KAINE SANADI*3️⃣

*WRITTEN BY:*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY:*
*KHALISAT HAYDAR*

*EDITTED BY:*
*SANAH S ISMA'IL MATAZU*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

Gaba d'aya kowa yabita da kallo dan da k'arfi tayi maganar, kuma da harshan turanci, shuru gayen yayi yana kallon ta da mamakin kalaman ta, shidai a iya sanin dayayi mata tsawon shekara biyu kenan suna tare a aji d'aya amman yasan takk'wala ce ta k'arshe, sam bata gane karatu da k'yar da sid'in goshi take wucewa kowace semester, dan haka ranshi bak'aramin baci yayi ba, ko uban wama yace mata da scholarship yazo makarantar oho mata, lallai zaiyi maganin ta kuwa.

Sam malamin baidamu da maganar datayi ba illa iyaka yace ma _Muhammad Hussein D'anbatta_ yaci gaba da maganar sa shi suke sauraro, a k'uffule yaci gaba da koro bayani tamkar zai fashe da kuka.

Haka sukaci gaba da d'aukar darasin har lokacin fitar shi yayi.

****

Yauma course d'in _Aliyu Rasheed Ganduje_ gare su, kamar koda yaushe d'akin karatun yacika ya batse, jiran shigowar sa kawai suke yi, Khadija ce ta dubi Amatullah tace, "yakama ta kije kiga Ganduje akan maganar test d'in ki,"
"eh yau d'in nan nake so inje daya fita zani,"
Basu k'arasa maganar ba, k'amshin sa ya tabbatar basu cewar ya iso, a hankali Amatullah ta furta, "barawon banza kawai!, wannan turaran dayake kuri dashi dagani kinsan satowa yayi kokuma maula yayi aka bashi!, dan wannan turaran yafi k'arfin albashin sa wallahi!," ta k'arasa maganar cike da takai ci, k"aramar dariya Khadija tasaki wanda yasata had'a ido da Aliyu wanda ya k'araso dai-dai gefen su dan hayewa sama.

Basarwa yayi ya haye sama dankuwa yau d'in nan saiya wulak'anta yarinyar nan acikin d'alibai y'an uwanta tunda ita batada mutunci, yasani sarai bata san komi ba inbanda gigiwan tsiya da rawar kai, dan haka yashiga yin abinda yakawo sa ajin.

Sanye yake cikin manyan kaya yayi bala'in yin k'yau tamkar asace a ruga, cikin k'warewa sosai yakeyi masu darasin, gaba d'aya Sun natsu suna saurarran sa.

Tsawon awa d'aya yana koyar dasu, kafin yashiga watso tambayoyi yana nuna wanda yakeso ya amsa, _Muhammad Hussein D'anbatta_ yasoma tadawa, nan ya bashi amsa ko gargada babu, dama yanasa ran hakan, yakuma yin wata tambayar ya nuna wata d'iyar turawa, itama ta mik'e ta bashi amsa kamar yanda ya buk'ata, daga k'arshe yayi wata tambayar ya nuna Amatullah wacce sam hankalin tama baya kansa yana kan wayar ta datake ta latse latse a ciki, Khadija nata d'an taba ta, amman ina hankalin ta yayi nisa, da k'arfi yakira sunan ta,

_Amatullahi Ahmad Fage!_
  Dasauri ta d'ago manyan idanuwan ta tana kallon sa, irin kallon ne mai d'auke da harara, mamakin yanda akai yasan sunan ta take, lallai ma gayen nan d'an rainin wayau ne!, sunana dana uba na yake kira haka kamar wata sa'ar shi? K'wafa taja dai-dai sanda yak'ara kiran sunan ta had'e da k'ara jefo mata tambayar tasa, tsaye ta mik'e kai tsaye tace "ban sani ba!, angaya maka ni k'aramar yarinyar ce daza ka tadani gaban y'ay'an talakawa kace in amsa wata banzan tambayar ka?"
"to wallahi Allah hawainiyar ka ta kiyayi rama ta!"
"ai dama tsiyar y'ay'an talakawa kenan, ni banma san meyasa aka d'auke ka aiki a wannan jami'ar ba, naga dai tuk turawa ne malaman amman kai bak'ikkirin k'azami dakai aka"....... Wani irin gigitaccan mari yasakar mata da hannunsa gaba da baya, sam batasan sakkowar shi ba, kawai saukar marin taji, bata gama watsakewa waba yakuma kai mata wani had'e da shak'eta yana fad'in "nine kazamin!?" hannunta yashiga ja da k'arfi yana k'ok'arin yin waje da ita sai tirjewa takeyi, a haka suka fito waje yana jaye da ita, nan danan guy's d'in ta suka yanyame shi kowanne d'auke da bindigar sa suka hayayyak'o masa tamkar zasu cinye shi.............

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*
[3/7, 11:14 AM] Fdaus Sodangi: *KAINE SANADI*4️⃣


*WRITTEN BY:*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY:*
*KHALISAT HAYDAR*

*EDITTED BY:*
*SANAH S. ISMA'IL MATAZU*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

Fisge hannun ta tayi cikin na sa da k'arfi tana kallon yanda wajan yayi jawur, murmushin takai ci ta yi sannan ta watsa masa manyan idanuwan ta, tace _"Aliyu Rasheed Ganduje"_ Kayi k'ok'ari matuk'a! Madallah da wannan k'arfi hali naka! Da har ka iya d'aga k'azamin hannun ka kasauke shi bisa wannan k'yak'yawan fuska tawa mai matuk'ar tsada! To ka bud'e manyan kunnuwan ka masu kama dana zomo ka saurare ni, wallahi wallahi wallahi Aliyu katabo ma kanka da y'an gidan ku kai da duka dangin ku bala'i da masifa, wanda wallahi nayi maka alk'awarin cewa zaman 9ja sai ya gagare ku, sai dai ku tafi can nijar dan da alama dama cirani yakawo ku 9ja dan da ganin wannan mummunar fuskar taka ansan y'an bararoji ne ku! Saboda haka ka zauna da shirin ka, "hmm! Inma banda k'addarar data hau kan ka ina kai ina taba _Amatullahi Ahmad fage!"_

"gaskiya ne kam d'an talaka bai iya samun waje ba, sai ya wuce gona da iri!"

Guy's d'in ta ne suka rufar masa ta d'aga masu hannu, cikin gadara da isa tace "ku k'yale shi, ak'wai sauran lokaci bayan zuba", wani k'ask'antaccan kallo tayi masa ta tofa masa miyau tace "kasaurare ni anjima inada magana da kai!,  daga haka ta juya abin ta tai gaba, guy's  d'in nata su ka rufa mata baya,  sororo Aliyu yayi yabisu da manyan idanuwansa da su ka kad'a jawur dasu, zuciyar sa wani irin k'una yake yi, jikin sa sai k'yar ma yake dan tsananin bacin rai, lallai yarinyar nan batasan _Aliyu Rasheed Ganduje_ ba!  Kamar shi wannan k'wailar yarinyar zata wulak'an ta haka?
Lallai watan cin uban ta ya tsaya, tunda iyayan nata basu yi mata tarbiyyar k'warai ba, "yazama dole in nuna mata ak'wai banbanci tsakanin mace da na miji!"
K'wafa yayi ya tafi yana tad'in zuci.

Wasu had'add'un motoci ne kuda hud'u masu azabar k'yau bak'ak'e wuluk dasu,  kowace mota a bayan ta an rubuta  _Amatullah_ suna isa gun motocin da sauri aka bud'e mata baya, tashiga ta kame tana daddan na wayar ta, d'aya ya shiga yaja motar yayin da sauran suka raba kansu, mota d'aya ce a gaba sai wanda take ciki a baya,  sai sauran biyun suka biyo su a baya da k'arfi suka fisgi motocin suka fice daga makarantar, yau kam Amatullah ta hakura da dukkan lectures d'in,
Kai tsaye gidan ta suka nufa wanda ke awajan makarantar, tsakanin makarantar ma da gidan nata yakai kilomita 5, wani d'an k'aramin gida ne mai azababban k'yau,  ya tsaru iya tsaruwa, taga ita sai k'awar ta _Khadija Muhammad Dala_ ke zama a cikin gidan sai kuwa tarin y'an aiki, harabar gidan cike yake da motoci iri iri, da sauri suka bud'e mata k'ofar motar ta fito, cikin tafiyar ta ta tak'ama tashiga cikin gidan,  da sauri y'ar aikin ta mai suna Teena ta iso gaban ta tare da zubewa tana k'wasar gaisuwa, da murmushi a fuskar ta ta amsa tana fad'in "babu matsala dai ko?"
"babu ranki ya dad'e,  meza a kawo maki?"
"bana buk'atar komi Teena, jeki abinki wanka ma zanyi yanzu,"
"to ranki ya dad'e bari inje inhad'a maki ruwan wankan,"
"ohh ohh Teena nace kibar shi kinaso kita saka ni magana" _sorry_ ranki ya dad'e,
D'uka da harshan turanci suke maganar kasancewar Teena baturiya ce babu hausa a bakin ta.

D'aki tashiga kai tsaye ta wuce toilet ta watsa ruwa tafito d'aure da tawul,  gaban dressing mirror ta wuce, ta yi tsaye tana k'arewa surar ta kallo,  iska ta shak'a cike da farin ciki, wani irin nishad'i takeji yanda ta gasa wa _Aliyu Ganduje_ magana cikin ruwan sanyi,  murmush tayi wanda yak'ara fitowa da k'yawun fuskar ta, a hankali ta furta "saina ga iyakar ka Aliyu Ganduje"
"ka tsokalowa kan ka tsuliyar dodo!"

Tafi minti sha biyar gaban madubin tana ta kalailaita,  tashafa wannan ta murza wancan ta fesa wannan ta gurza wancan, ahaka dai har ta gama,  ta sanya wata had'add'iyar doguwar riga, ta fice daga d'akin kanta ko d'an k'wali babu sai wata y'ar k'aramar waya mai k'yau a hannun ta.
Palo ta shiga ta kame a d'aya daga cikin had'addun kujerun dake cikin palon, tana lallatsa

wayar,
Teena ce tafito tace "ranki ya dad'e har kin fito?"
Kai kawai ta d'aga mata kafin tace "kije kice ma musa yatafi makaranta yajira Khadija idan ta gama ya maido ta gida"
"to ranki ya dad'e"

Da sauri Teena ta fice dan isar da sak'on uwar d'akin ta...........

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI*5to10

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*EDITTED BY*
*SANAH S, ISMA'IL MATAZU*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

_ina matuk'ar jin dad'in yabawar ku agareni tare da k'arfafa min guiwa, nogode sosai da k'aunar ku agare ni domin duk mai son abin ka to kai yake so._

_Fatyma Izland_
_Ummi Hambali_
_Fatima Aliyu Garba_
_Zara Bukkar_
_Humaira Bashir Melody_

Wani irin mugun kallo yake mata ko k'yaftawa baya yi, jikin sa gaba d'aya rawa yake yi idanuwansa sun kad'a sunyi jawur kamar gauta.
A sanyaye tasaki hannun nasa tare dayin baya kad'an, matsowa yasoma yi inda take cikin wani irin taku, zuciyar ta ce tayi wani irin bugawa nan da nan kamannin ta ya canza alamar tsoro yad'an baiyya na a fuskar ta amman cikin dakiya irin tata ta dake saidai tasoma yin baya kad'an kad'an, binta yaciga dayi har ta kurema bango, tamkar zai shige cikin jikin ta yaja ya tsaya yai mata runfa da makeken k'irjin sa.
Yafita tsawo nesa ba kusa ba da ace wani zai shigo a lokacin sam bazai yi nasarar ganin taba domin kuwa gaba d'aya _Aliyu Rasheed Ganduje_ ya lullube ta da tsawon sa dakuma fad'in sa.
Bud'e bakinsa yayi zai mata magana wani irin had'add'an k'amshi had'e dawani irin huci mai zafin gaske yabigi fuskar ta, nan da nan y'an hanjin ta suka kad'a zuciyar ta ta yanke ta fad'i rass!! Rass!!
Manyan idanuwan ta ta zaro tana duban sa tsoro k'arara shimfid'e a fuskar tata.

Cikin wani irin kakkausar murya yashi ga fad'in "meyasa kika rainani dayawa har kike tunanin zaki iya siyan _Aliyu Rasheed Ganduje?"_
"me kike tak'ama dashi?"
"wacece ke mekike da shi?"
"kinyi babban kuskure dakika shiga gonar _Aliyu Rasheed Ganduje_ kin tafka babban kuskure da kika shigo rayuwar Aliyu".

"Da ace zaki nimawa kanki gata dakin tattara tsummo karanki kin bar k'asar nan dan zamanki baida wani amfani, kina zaman kashe wando ne zaman dazai sa ki koma abin tausayi abin k'watance acikin makarantar nan!".

"ina jin dad'in wannan game d'in damuke bugawa nida ke! Dan haka Allah yabawa mai rabo sa'a ,kina iya ficewa daga _office_ d'ina Kafin in rufe idona in bud'e, idan kuwa ba haka ba na rantse da Allah saina illata ki anan yanzu ba anjima ba idan kuma k'aramar k'wak'walwar ki yabaki k'arya nakeyi ki tsaya in bud'e ido baki fice ba kigani."

Tsaki taja tare da fad'in "zamu had'u ne zakasha mamaki wallahi wallahi!".

Dasauri ta d'au jakarta tafice.

Tana fituwa suka gwabza karo ita da _Muhammad Hussein D'anbatta_ d'auke yake dawasu littafai a hannun sa, yayinda itama take rik'e da jakar ta, littafan nashi ne suka watse a gaban ta, yayin da itama jak'ar nata ya fad'i k'asa daf da littafan.

Gaba d'ayan su suka d'uk'a lokaci d'aya kowanne ya d'auki nasa.

Tana d'agowa bud'an bakin ta tace "shishigi da niman suna! To uban me kuma kazo yi a _office_ d'innan?"
"Dad'i na da d'an talaka wallahi bai iya samun waje ba!, mutum shi ba d'an kowa ba, asalima d'an scholarship, amman sai iyayin tsiya da fi'ili."

"yanzu in banda jahilci da duhun kai irin na d'an k'auye ina kai ina bangaza ta, _Hussein D'anbatta_ kake ko uban wa?"

"To bari ingaya maka ninan daka ganni bana yafiya!, bana mantuwa!, haka nan kuma bana mance ranar d'aukar fansa!"

"Dan haka kazauna cikin shiri wannan lallausar jikin daka bangaza bazai wuce a banza ba saina nuna maka kuran ka!"

Taja wani mugun tsaki da k'wafa tamkar harshan ta zai bar bakin ta tayi gaba guy's d'in ta suka rufa mata baya.

Mamakin kalaman ta suka sa shi sakin baki yana duban ta, lallai yarinyar nan y'ar rainin hankali ce yafad'i a fili, hmm! Adai guji zuwa rafi.....

Khadija ce ta dube ta bayan ta zauna tace "to ya kukayi da mutumin naki?"
Iska ta furzar cikin bacin rai tace "ai kin san komi akai da jakki sai yaci kara!"
Nayi iya k'ok'ari na amman abin ya faskara,
Kinsan shi taurin kai gare shi da girman kai kamar shaid'an.
Dariya Khadija ta k'washe dashi harda tuntsurawa.
"To Amatullah yanzu yaza mu bullo masa ne"
"amman kinsan me nifa wallahi guy d'in burge ni yake yi dan ya iya d'aukar wanka k'arshe wallahi."

Wani irin mugun kallo Amatullah tayi mata cikin daka tsawa tace "kar ki k'ara batan rai dan Allah!"
"meye abin burgewa ajikin wannan d'an matsiyatan?"

Kisa ido kigani muna nan za a zo a damk'i shege dan da ganin kayan daya ke sawa yana fafa dasu da turaran dayake amfani kinsan katon barawo ne! Dan haka ina nan ina addu'a ina kaiwa Allah kuka na Allah ya kawo k'arshan sa watau watan cin uban sa ya kama a damk'i matsiyacin mai kama da k'osan rogo.

Hmm! Amatullahi kenan inaso inga ranan da wannan kiyayya taku zata k'are, koda yake shima guy d'in ne d'an rainin wayau Allah!.

**************

Bayan sati d'aya yauma kamar kullum Amatullah taki ta shirya da wuri dan sanin cewa yau lecture d'in farko ta _Aliyu Ganduje_ ce, tana ji tana gani Khadija ta shirya ta wuce abin ta, ita kuwa sai bayan minti arba'in da yafiyar ta sannan ta shirya ta Shiga makarantar ita da guy's d'in ta.
Kai tsaye tashiga cikin ajin tana takun ta ta tak'ama, gaba d'aya k'amshin ta ya bad'e ko ina.
Cingum take tauna abin ta cike da yanga,
Sosai ya bud'e murya yace "karki k'araso nan! Koma inda kika fito,"
Ko kalma d'aya bata furta ba asali ma ko tsakin bata yi ba yau, ta juye tayi waje tana wani jujjuya jiki.

Cikin bacin rai yaci gaba da koyar da darasin sa.

Kai tsaye _office_ d'in shugaban makarantar ta nufa kanta tsaye ta fad'a _office_ d'in.
Zaune yake shida wasu manyan makarantar suna d'an tattaunawa.
Cike da fara'a gaba d'ayan su suka mik'e suka tare ta saikace ita ce shgabar k'asar.
Cikin fara'a shugaban makarantar yasoma fad'in "ranki ya dad'e da kanki da sassafen nan lafiya dai ko?"
Kuka ta fashe dashi sosai tana fad'in su kira Abban ta su shaida masa bazasu iya d'aukar amanar daya basu ba nata, wanda harda mak'udan kud'ad'e ya had'a masu dan dai kurum su kular masa da ita....... Da sauri shugaban makarantar ya katseta a rud'e da fad'in me akai mata?
 Cikin kuka da shasshek'a tasoma magana.
_Aliyu Rasheed Ganduje ya tsane ni acikin makarantar nan, sam baya son ci gaba na,  baya son farincikina da k'wanciyar hankali na.
Kullum burin shi shine yatakurawa rayuwata.
Nashigo makaranta _last two weeks_ ya kore ni daga ajin sa, yaba da test bani,  yace duk wanda baiyi test d'in shi ba bazai ci jarabawar saba.
Nabishi _office_ d'in sa nabashi hakuri yace sai dai in siya test d'in da kud'i,  na bashi kud'i masu yawa yace shikenan magana ta k'are.
_last week_ yakira ni _office_ d'in sa bayan naje yake cemin shi ya janye zancan kud'i saidai inbashi kaina,  tak'ara fashewa da kuka mai cin rai duk wanda yagan ta a lokacin sai ya tausaya mata."

"ina son karatuna sosai saboda burin mahaifinane insamu ilimi sosai kuma kun sani, wannan dalili yasa nabawa _Aliyu Rasheed Ganduje kai na saboda kawai yadai bani test d'in nan kada infad'i jarabawar sa."

"A bin mamaki yau ya tare ni dazancan saidai in k'ara bashi kaina saboda test d'in nan ba abu bane mai sauk'i dazai iya bani shi haka a bagas."

"na nuna masa sam ban yarda ba tunda abin nasa rainin hankali ne shine wai dan nashiga lecture d'in shi yanzu ya koreni daga ajin, tak'ara fashewa da wani irin kuka tamkar zata

shid'e...........

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI*1️⃣0️⃣to1️⃣5️⃣

*WRITTEN BY:*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY:*
*KHALISAT HAYDAR*

*EDITTED BY:*
*SANAH S, ISMA'IL MATAZU*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

_wannan page d'in nakune_

_Anty Sadiya Jegal_
_Safreenah Annour_
_Abeeda_

A fusace shugaban makarantar yace _"what!_ dama duk cikin turan ci suke maganar, yaci gaba da fad'in _Aliyu Rasheed Ganduje_ ne ya aikata wannan mummunar..... D'aya daga cikin wa'yan da yake tare dasu ne ya katse shi da fad'in karkayi mamaki zai aikata fiye da hakan! Ai d'an iskan yarone ak'wai yarinyar data taba kawo min k'arar sa nida kaina naja masa kunni aka rufe maganar to kaga yanzu yakuma maimaitawa inda bazamu taba k'yale shiba!,

_(kai jama'a kuji k'arya k'iri-k'iri)_

Cikin muryar kuka tace "idan ma baku yarda da zance naba muje ajin a tambaye su, domin kuwa su shaida ne, suna kallo ya kore ni rannan yayi test, yau ma suna kallo yakore ni, har marina yayi rannan duk agaban kowa akayi nasan zasu fad'i gaskiya, sannan kuma _Muhammad Hussein D'anbatta_ shaida nane, domin kuwa yaga fito wata daga _office_ d'in _Aliyu Rasheed Ganduje_ ranan dana kai masa kud'i.

A fusace shugabar makarantar ya tasata gaba ita da sauran malaman suka nufi _department_ d'in nasu, kai tsaye ajin suka nufa ,
Yana ta koyar wa abin shi cikin k'wanciyar hankali da k'warewa.
Koda ya hango su baisa ya tsaya daga abinda yake ba illama k'ara sautin shi dayayi wajan baya nin daya keyi.

Saida suka k'araso har gaban ajin sannan Aliyu yayi shuru yana duban su.
Shugaban makarantar ne yafara magana a fusace bayan ya fuskan ci y'an ajin, "yau shene kukayi test d'in _Aliyu Ganduje?"_ yayi tambayar cikin dakakkiyar murya da harshan turanci.
Gaba d'aya suka had'a baki suka sanar dashi.
Kai ya gwad'a kafin yace "kunsan wanna?" yanuna Amatullah, suka bashi amsa dacewa nan ajin take, yace "a ranan da Aliyu yayi test d'in sa ya kori Amatullah kokuwa?"
Suka sake bashi amsa da tabbas anyi haka, yakore ta sannan daga baya yarubuta masu test.
Yasake cewa "yau tashigo ajin nan kobata shigo ba?"
Suka sake bashi amsa dacewa tashigo yakore ta saboda dama shi k'a'idar sa indai yariga ka shigowa to koran ka zaiyi.
_"where is Muhammad Hussein D'anbatta?"_
Mik'ewa yayi tare da fad'in _"am here sir!"_

"inaso in tambaye ka tsakanin ka da Allah zaka gaya min, idan ka boye min kokari min k'arya baza ka boyewa Allah ba saboda yana kallon ka!".

Kai _Muhammad Hussein D'anbatta_ ya d'aga masa alamar zai fad'i gaskiya.
"kataba ganin wannan y'ar ajin taku tafito daga _office_ d'in _Aliyu Ganduje_ ko za ta shiga?"

Shuru Muhammad yayi tsawon wani lokaci shidai bai san make faruwa ba amman tabbas dai yasan ya taba ganin ta tafito harma ta gaggaya masa bak'ak'en maganganu, wanda har gobe sunai masa ciwo matuk'a.
Dan haka yace "k'warai kuwa idan ban manta ba anyi sati d'aya kenan dana ganta tafito daga _office_ d'in _Aliyu Ganduje_
_"good"_
Shugaban makarantar ya furta da k'arfi, sannan ya dubi Aliyu wanda yayi sororo yana kallon sa, zuciyar sa yana tafasa meyake shirin gani haka yau?
Kamar shi shi _Aliyu Rasheed Ganduje_ za a wulak'anta a cikin yara k'anana! Way'anda suke ganin girman sa da mutuncin sa!?

Lallai yarinyar nan ta d'auko ruwan dafa kanta yau!

Wani mugun kallo shugaban makarantar yayi masa kafin yafara magana cikin masifa, "dama nasan cewa baza ta yi maka k'arya ba, domin d'an babban gida baya k'arya!, kawai nazo ne dan in fita hakkin ka ayi komi a gaban ka kana gani dan kar kace anyima sharri ko k'azafi!.
Ya kalli Amatullahi yace "ranki ya dad'e maimata abinda ya had'aku agaban sa yaji dan yasan komi ya iso kunnin mu, kuma dama yasan dokar makarantar nan dan haka sai ya yankewa kansa hukunci da kansa.

Babu kunya babu tsoron Allah Amatullah ta maimaita abinda tace masu babu ragi babu k'ari.
Shugaban makarantar ya dubi Aliyu yace "meza ka iya cewa akan abinda ta fad'a?"
Bud'an bakin Aliyu sai cewa yayi gaskiya ta fad'a anyi haka.
"murmush Amatullah tayi tace ai bai isa ya k'aryata ba tunda yasan cewa tabbas ya aikata.
Wani irin kallo Aliyu yake mata cikin ido mai wuyar fassarawa, gira ta d'aga masa ta kashe masa ido d'aya.

"to Aliyu Ganduje kana iya zuwa _office_ d'ina domin ka amshi takardar sallama, domin kaima kasani wannan shine hukun cin duk wanda aka kama da irin laifin ka.
Daga haka suka fice gaba d'ayan su har Amatullah tabi su tana karkad'a mazaunai.

Kaf miyan bakin Aliyu ya kafi da k'yar ya iya tattaro numfashin sa gu d'aya har ya saisai ta kansa.
Idanuwan sa sam babu k'yawun gani.
Cikin wani irin tafiya mai kama dana bijimin sa yafice daga cikin ajin.
Gaba d'aya d'aliban jikin su yayi sanyi da ace sun san wannan ne dalilin da yasa akai masu tambayoyi ai da basu fad'i komi ba sun rufa masa asiri domin kuwa koba komi suna gane lectures d'in sa.

Khadija kuwa hawaye ne taji yana gudu bisa fuskar ta wanda ita kan ta batasan dalilin saukar suba.

*******

Bayan awa biyar, Amatullah ce ta k'ure k'arar radio tana shan sauti tana tik'ar rawa daga ita sai wata yar _vest_ da guntun wando.
Rawa take hankalin ta k'wance dagani kasan tana cikin nishad'i, wani irin rawa take tamkar zata karye, sai kace wata bebin roba.

Khadija ce tayi sallama tashigo amman sam Amatullah bata san da shigowar taba.
Khadija tafi minti biyar da shigowa amman sam Amatullah tayi nisa a sharholiyar ta.
Wani irin juyi tayi cikin rawar ta kawai sukai ido hud'u da aminiyar ta Khadija.
Dasauri ta kashe radio d'in cikin ihun murna ta rungume Khadija tana fad'in _i am the winner of

the game_ sis kitayani murna, nagama da _Aliyu Rasheed Ganduje_ nagama dashi wallahi.

"Yau ina cikin farin ciki mara misaltuwa,  Allah nagode maka daka bani sa'a akan mak'iyina."
  "Khadija na dad'e banyi farinciki irin na yau ba wallahi,"
Na maida Aliyu abin kwatan ce a duniya,
"yace wai in tattara tsummokarana in koma k'asata."
"to gashi nan kafin ni in koma matsiyacin ya riga ni."
"hmm!! Ai duk wanda yaci tuwo dani wallahi Allah miya yasha!"
"in banda _Aliyu Rasheed Ganduje_ ina shi ina ja da d'iyar manya!"

"ai bigi sai big! Babban goro sai magogin k'arfe!"
"Hmm!!  _Aliyu Rasheed Ganduje_ *KAINE SANADI*
amman sam bahaka Amatullah take ba, kaine ka canza ni nazama haka.

Sai a lokacin ta lura da yanda Aminiyar tata ta tsaya mata cak tamkar wata gunki bata taya ta farin ciki.
Jiki a sanyaye ta sake ta tanai mata kallon tuhuma.
"Khadija lafiyar ki kuwa?"
Cikin muryar kuka Khadija tasoma magana, "Amatullah sam banji dad'in abinda kikai ma Aliyu ba!  Sam baki k'yauta ba."
"ina so ki sani Allah ya jarabceni da k'aunar _Aliyu Rasheed Ganduje_ tun daga ranan dana soma ganin sa!"
"ina son Aliyu ina k'aunar sa ina kuma burin in mallake sa,  sai gashi cikin k'ank'anin lokaci kin rusa min lissafi na!  Amatullah  bakiyi min adalci ba kin ma rayuwata illa babba!, yanzu ta ina zani niman Aliyu ina zanbi ingan sa, dawani ido zan dube sa?" tafashe dawani irin kuka mai taba zuciyar mai saurare.

Wani irin kallo Amatullah keyi mata ko k'yaftawa batayi, kafin tafara magana cikin rashin mutunci mai cike da masifa.
"Khadija ashe bakida mutunci bansani ba! Ashe zaune nake da makiyiya ta bansani ba?"
"haba! Tabbas biri yayi kama da mutum."
"lallai d'an adam butulu ne"
"to bud'e kunnuwan ki kiji ni da k'yau!  Daga yau sai yau,  bani baki!  Ke ko a hanya kika ganni kika nuna kinsan ni Allah ya isa ban yafe maki ba!  Kuma ki tattara kayan ki kibar min gida na yan zunnan bada bata lokaci ba"
"banza mara zuciya!  Inbanda Kare ya cinye zuciyar ki ina ke ina Aliyu Ganduje?"
"mutumin daya tsane mu nida ke baya k'aunar ya bud'e ido yagan mu a duniya!  Wai shi kike k'auna!  To ki k'arawa motar ki mai kibi Aliyu Ganduje gidan matsiyacin uban sa yayi maki wajan k'wana acan."

Taja tsaki tanimi kujera ta kame tana ci gaba da masifa.........

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI* 1️⃣6️⃣

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*EDITTED BY*
*SANAH S, ISMA'IL MATAZU*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

_kuyi hakuri da wannan ina fama da ciwon ido, ina barar addu'ar ku pls_

Sororo Khadija tayi tana kallon Amatullah tana jinjina irin rashin mutuncin ta, sam bata zaci hakan daga gare ta ta, zuciyar ta na k'una ta zaro wayar ta cikin jaka ta shiga latsa wasu lambobi ta kara a kunnin ta tanufi d'akin k'wanar su.
Magana ta d'anyi nawasu y'an dak'ik'u sannan ta kashe wayar tashiga had'a kayan ta, duk wani abu datasan nata ne sai da ta d'auki abinta ta saka cikin jaka, tsawon minti talatin ta d'auka tana tattara kayan ta, kafin wayar ta dake gefen ta yashiga niman agaji, hannu tasa ta d'auka, ta d'an yi magana sannan ta kashe ta nufi palo.
har zuwa wannan lokacin Amatullah na k'wance bisa kujera yanda ta barta, kallo d'aya tayi mata ta kauda kai tace "ki gyara maza zasu shigo".

Wani irin kallon banza tayi mata tace "bangane maza zasu shigo ba, uban me zai shigo dawasu k'arti gidan nan?".
Bata bari Khadija ta bata amsa ba taci gaba da fad'in "to mawai tsirara nake da zaki wani ce in gyara maza zasu shugo sai kace irin kin ganni zindir d'in nan!". Tayi k'wafa ta maida kanta ta k'wanta.
Khadija bata ce mata komi ba illa waje da ta fice batafi minti biyu ba sai ga ta dawasu gardawan maza har su uku kai tsaye tashige da su d'akin suka jido mata kayan ta suka fita dashi suka sa a motar da suka zo dashi. Khadija ta kalli Amatullah tace "ranki ya dad'e _Amatullah Ahmad Fage_ _Khadija Muhammad Dala_ zata bar maki gidan ki a yanzu basai anjima ba! Ke k'asar ma gaba d'aya zata bar maki! Dan Khadija bazata iya zama inuwa d'aya da ke ba, so zan k'oma k'asar danafi wayau watau k'asar haihuwa ta, in da babu shegen da ya isa yace Khadija tattara kayan ki!, ke kuma da kika yankewa k'asar cibi sai kici gaba da zama har abada, sannan kuma ina baki shawara da kibi duniya a hankali, idan mune yau bamune gobe ba, kirage girman kai da wulakanta mutane, kirage isa da nuna takama, ki koyi iya zama da mutane ki koyi yin biyayya dana gaba dake, wannan ita ce nasihata a gare ki _Amatullah Ahmad Fage_ daga haka ta fice abin ta ko waiwaye babu, wani mahaukacin tsaki Amatullah ta ja tare da fad'in "aikin banza aikin wofi! Dan kin bar k'asar da karatun ki sai me! Asarar wa! Ai kanki kikai mawa banza shasha sha wacce bata san inda keyi mata ciwo ba, in banda rashin sanin ciwon kai akan wani k'ato har zaki bar karatun ki?"
"Lallai yarinyar nan bata da mafad'i ko ince tasamu shashashun iyaye! Ni yanzu na isa in komawa Abba ince banyin karatu saboda wani shege? Buhun uba lallai ma, ai wallahi wargi wuri yasamu.
Gaba d'aya ranta yagama baci duk farincikin data ke ciki d'azu yanzu yakoma bak'in ciki dan haka ta min'e a fusace ta Shiga d'aki ta ciro wata had'add'iyar _after_ ta sanya akan d'an iskan shigar jikin ta ta yane kanta da d'an mayafin ta figi mukullin mota tayi waje, guy's d'in ta suka iso da sauri suna tambayar ta dawusu motocin za ta fita dasu? Hannu ta d'aga masu a hankali tace kuyi zaman ku ni d'aya zan fita! Tsoro ne ya baiyana a fuskokin su, cikin k'arfin hali d'aya yace ranki ya dad'e kibari akai ki koba mu duka ba ko mutum uku ne, harara ta watsa masa tayi tafiyar ta.

Kai tsaye wani gun shak'atawa ta nufa inda kowa ke harkar gaban sa, nan tasa a ka kawo mata _ice cream_ ta shiga sha a hankali tana samun natsuwa, tafi awa d'aya a gun tana huta wa kafin ta biyasu ta shiga motar ta ta fisge shi da k'arfi tayi gaba abin ta, tunda ta fito daga gun shak'atawar ta lura dawata mota na biye da ita a baya, rage gudun motar nata tayi dan wancen yazo ya wuce amman da mamakin ta saima motar yazo ya sha gaban ta,
Wani irin tsoro ne yashige ta hankalin ta yayi bala'in tashi, da k'yar ta iya tsaida motar saura kad'an ya bugi d'ayan motar........

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*

[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI* 16to20

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

_*ALHAMDULILLAH NAJI SAUKI SOSAI, NAGODE KWARAI DA KULAWAR KU A GARE NI MASOYANA NAGODE SOSAI, HAKIKA NAJI DADIN YANDA NAITA GANIN SAKONNIN KU KUNAYI MIN FATAN SAMUN LAFIYA, HARDA MA MASU KIRA NA HAKAN YANUNA MIN LALLAI KUNA KAUNATA SABODA ALLAH, BANIDA ABINDA ZANCE SAIDAI INCE INA MAKU FATAN ALKAIRI MASOYAN SODANGI*

_wannan shafin naki ne masoyiyar asali nagode sosai da taimakon ki agare ni..._

_Fatima Aliyu Garba_

Bata k'arasa rikicewa ba sai da ta ga wani k'arfaffan mutum ya fito daga motar hannun sa d'auke da bindiga fuskar sa sanye da safar fuska. Kai tsaye motar ta yaiwa tsinke, bud'ewa yayi da k'arfi ya finciko ta cikin harshen turanci yace idan kikai min ihu saina fasa k'ok'on kanki da bindigar nan!.

Jikin ta ne ya d'auki rawa tamkar mazari kiris yarage ta saki fitsari, a haka ya tura ta a tasa motar ya rufe ya shiga yaja da gudu yabar wurin, gudu yake ta shararawa tamkar zasu tashi sama inbanda kuka da hawaye babu abin da Amatullah keyi dan babu damar ihu tana tsoron ya halbe kanta kamar yadda yace, shikenan yau ita nata ya k'are tasan kashe ta zaiyi, addu'a take ta yi babu kakkautawa.

Saida sukayi tafiyar minti ashirin kafin suka iso wata unguwa, shuru babu kowa y'an gida jan gun ma basu wuce biyar ba.

Da k'arfi ya fisgo ta tana ciccijewa ya sabe ta kamar wata y'ar tsana yayi ciki da ita kai tsaye wani makeken  bedroom dake cikin gidan yayi da ita.

Kuka takeyi tana bugun sa da hannayan ta duka biyun, amman tamkar dutse take bugu babu alamar yana ji, wayyo na shiga uku ni Amatullah zai kashe ni!.

Wani gigitaccan mari yasakar mata wanda sai da taga taurari. ihu tasaki tare da fad'uwa kasa tana rok'on shi ya k'yale ta kada ya kasheta,
"Bawan Allah wallahi Allah ko nawa kakeso babana zai baka amman kada ka kashe ni dan girman Allah".... ..
bata k'arasa ba ya fisgo ta tare da jan gashinta har sai da gyalen kanta ya fadi k'asa,
tana dagowa yana zare mask din dake fuskar shi wazata gani?
_Aliyu Rashid Ganduje_ Cikin tane yayi wani irin kuwwa tare da juyi tamkar y'ayan hanjin ta zasu yo waje.
Cikin hanzari ta mik'e tayi baya tana nuna shi da d'an yatsan ta sai kuma ta k'washe da dariya tana fad'in "kai sakarai dan talaka mara galihu!
kai har ka isa naji tsoron ka?"
" ko kana tunanin wai in kayi hakan zanji tsoro ne?"
" to wallahi kayi kad'an, wawa d'an iska kawai!

Wani irin kukan kura Aliyu yayi, yayi k'wallo da ita da k'arfi ta fad'a jikin gado ya bita ya kamota.
"yau zan nuna maki waye _Aliyu Rashid Ganduje_ dan ubanki."
ya hau gadon tare da jawota da k'arfi, bigeshi tayi tana fad'in "kai meye haka zaka sa kazamin hannunka ajiki na?"
murmushi yayi wanda shi kad'ai yasan ma'anar shi.
tsaki yaja yace, "uban meye a jikin naki da har za'a taba?"
"yau zaki san kinzo hannuna zan nuna maki lallai akwai banbanci tsakanin mace da na miji!
Rigar ta ya fara ja tana rikewa tare da d'ura masa ashar, bakin nata yaima k'yakkyawan bugu ya murd'e hannun ta baya ya cire rigar yayi jifa da ita, nan da nan Aliyu ya razana da ganin surarta dama bra da y'ar vest d'in jikin ta ne kawai sai kuwa bumb short dake jikin ta dama sai tasa after dress a sama.
Basar wa yayi cike da k'arfin hali amman yakasa kauda idon sa akan ta.

hankali tashe take kallonsa amma bata so ta nuna taji tsoro,  sai ta dake tana hararrarsa, "wai kai mahaukaci ne daza ka cire min riga ai wannan iskanci ne"
bata k'arasa ba sakamakon buga ta da yayi a kan gado a take kan ta ya fashe ta saki wani razanannen ihu tana kallonsa da idanuwan ta dasukayo waje duka,
jawota ya karayi ta fad'o k'asa a gigice ta ke kallonsa, mari yak'ara sakar mata yace
"kallo na na kawo ki kiyi?"
da sauri ta d'ukar da kanta dan wani irin bala'in taoron shi ne yashige ta babu shiri.
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: Wasa wasa saiga the great _Amatullah Ahmad Fage_ a gaban _Aliyu Rasheed Ganduje_ da ta raina tana  rok'on sa da yayi hakuri ya k'yale ta bazata iya frog jump ba daya sata.

Wani irin kallon wulakanci yayi mata, "yace kitashi kifara wallahi tun kafin nayi k'wallo dake!"
kallon shi ta tsayi tanayi hawaye na gudu bisa fuskar ta, taya ma zaice wai tayi frog jump! itada ko kneel down bata taba yi ba, inba yanzu da yasata ba, kuma wallahi ko kasheta zai bazata yi ba.
"haba Aliyu! tayama ya zaka kalle ni kace nayi frog jump! ko kaga kalar wahala a tare dani ne?"
"danma kasamu ina rokonka!?"

jifa yayi da ita kan gado ya dakko zabgegiyar dorina yayo kanta,
A gigice ta mik'e jikin ta na rawa tasoma yin tsallan k'wad'on, tana fad'in, "dan Allah kayi hakuri wlallahi bazan k'ara shiga harkar ka ba plz kada ka dakeni.

A tsorace take maganar tana kuka dan ba a bunda ta tsana daya wuce a taba mata lafiyar jikinta,
bai bi ta kanta ba ya fara zabga mata bulala baji ba gani.
ihu take tana neman taimako amma bai k'yale ta ba sai da yai mata dankaren duka duk ya farfasa mata jikinta har sai data suma dan azaba,
Da sauri yayo kanta hankali a tashe yana tunanin ko kasheta yayi, da sauri yaje ya dakko ruwa a fridge ya zuba mata.

a gigice ta farka tana rokon sa ya k'yaleta hakanan bazata k'ara ba.
Wani mugun harara ya watsa mata ya ce, "har yanzu baki gama sanin kala taba tunda bakin ki bai mutu ba!"
So nike kisan koni waye! "dan iskanci har ni zaki kalla ni Aliyu Rashid ki kirani da talaka d'an iska ko?"
" to yau zaki san ni dan iska ne na k'arshe,"
kanta yayi ta saki ihu tana kuka "dan Allah na rokeka kar ka lalata man rayuwa natuba ba zan k'araba wallahi Allah!"
yace "a she ke karamar yar iska ce banza wadda bata san ciwon kanta ba!
Gaba d'aya ya fisgota jikin sa ya balle bra d'in jikin ta yayi ma k''irjin ta kyakkyawan damka da duka hannayan sa, cikin tsabagen mugunta da son zuciya yashiga matsasu da iya k'arfin sa yana wani lumshe ido, ihu tasaki sosai saboda azabar zafi da kidimewa,
Bakinsa yakai a kansu yasoma yimasu shan Allah tsine tuni Amatullah tafita haiyyacin ta ta sume masa, sam baisan ta suma ba sai murzan ta yake son ransa,
Tsawon wani lokaci yana abu d'aya kafin yacire bakin sa, tuni sunyi jawur saboda muguntar dayayi masu, sai a lokacin ya kula suma ta kuma yi, ruwa yakuma d'aukowa ya k'wara mata.
Wani ajiyar zuciya mai k'arfi tasaki tare da sakin ihu dan yanda taji k'irjin ta tamkar zai cire dan azaba.
Ido hudu sukai dashi yana mata wani irin kallo, baki ta bude cikin zubar hawaye tace Aliyu.. Bai bari ta furta ba ya had'e bakin sa da nata cikin mugunta yake shan bakin daga k'arshe ya gantsara mata cizo a harshe kiris yarage bata shide ba dan azaba.
A fusace yashiga fadin Amatullah baki kai matsayin wadda Aliyu Rashid zai hada jiki da ita ba dan ni kin man kadan wallahi! Dube kifa! kwaila dake! ba ki da abunda ma zaki burge wani namiji dashi,

Kuka mai k'arfi tasaki  tana tunanin inama ta mutu akan wannan bakin ciki da Aliyu ya samata.

Ita ai gara ma bugun da yai mata akan ya kirata da kwaila wai har ita zaice ma bata da abunda zata burge maza.
Wani wawan tsawa ya daka mata yace tashi tsaye!
Kuka takuma Saki tana tunanin yanda zata mike a haka babu bra a jikin ta, tsawa yakuma daka mata wanda yasata mikewa a rikice bata shirya ba.

Oya tsalle zaki yi sau d'ari ina kallon ki kuma idan kika tsaya ko na minti daya ne saikin sake daga farko wallahi kinji na rantse maki!
Kuka take sosai gaskiya Aliyu ba karamin tsinanne bane take fadi a zuciyar ta.
Ke nake jira!  Yafadi a fusace,  tana ji tana gani tafara daka tsalle Aliyu ya kurawa kirjin ta ido yana kallo,  runtse ido tayi cike da takai ci tana tunanin irin abinda zatayiwa Aliyu Ganduje.

Aliyu ne tsaye kanta yana magana cikin daga murya "wai ke ga mai kud'i ko?"
"to ni tunda nake ban taba ganin k'askantaccen  talaka kamar ki ba!
"ke har kina tunanin akwai kud'in da zaki iya bani ko?"
 "to bari kiji kinga wannan rigar ta jikina?"
Ya fadi yana nunawa da hannunsa, "wannan rigar tawa d'aya zata sayi duka zuri'arku",
"Jibe ki! matsiyaciya mai kama da namun daji"!......

_To masu karatu kundai san ido ba abin wasa bane so zandan dagawa typing kafa, zan ringa yin tsallaken kwana daya daya idan nayi yau bazanyi gobe ba saboda lafiyar ido na so kubiyo ni jibi idan Allah ya kaimu rai da lafiya,  daga alkalamin yar mutan Sodangi._

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI* 20to25

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

_wannan page d'in nakine_ *ANTY SIS*  _nagode da kulawar ki._

_Zanyi amfani da wannan damar in mik'a sak'on godiya ta ga mutanan dasuka kirani danjin lafiyar jikina haka kuma in bawa wayan da sukai min message ta whatsapp hakuri dan rashin reply dina hakan yafaru ne dalilin yawan messages d'in da na zo na iske dayawa, amman ina niman afuwan ku na gode da kulawar ku a gare ni Sodangi tana Godiya kwarai da gaske_

Kuka Amatullah keyi tamkar ranta zai fita, ba k'aramin wulakanci Aliyu yayi mata ba kafin ya k'yale ta ta maida kayan ta. Kasa tafiya tayi a haka yaja ta har cikin motar sa ya maida ta gun motar ta ya jata ya tura ta ciki ya dube ta a wulak'ance yace "ki saurare ni a kashi na biyu dan wannan sharan fage ne, shafin farko ne muka bud'e, ki saurari abinda zai biyo baya, kina iya d'aukar mata ki kinji y'an mata yafad'i had'e da kashe mata ido d'aya.

Harara ta watsa masa tana hawaye, Murmushi yayi yace _"bye sai mun had'u kinji y'ar matsiyata!_"

Ya wuce yabar ta nan tana kuka da sak'e-sak'e.

Dak'yar ta iya d'aga wayar ta takira guy's d'in ta ta fad'i masu inda take.

Minti goma kacal sai gasu zuga guda, cikin tashin hankali suke tambayar ta abinda ke faruwa, batace masu komi ba illa baya data koma da k'yar cike da k'arfin hali.

A haka suka isa gidan cike da tashin hankali, wani irin kallo tayi masu kafin tace "bana son inji kowace magana daga bakin kowa".

Tana fad'in haka ta sauka bayan sun bud'e mata k'ofa ta shige gidan a d'aki ta zube bisa gado tana wani irin kuka abin tausayi, da k'yar ta iya shiga band'aki ta gasa jikin ta sosai,  tanayi tana kuka.

D'aure da tawul ta fito daga band'akin ta fad'a gado nan da nan bacci yayi awon gaba da ita.

**************

K'wanan Amatullah uku a gida bata fita ko ina, zazzabi mai zafin gaske take fama dashi amman ta ki yarda a kaita asibiti kuma taki yarda a kira likita gida ya duba ta.

Yauma k'wance take a palo tana rawar sanyi Teena mai aikin ta na duk'e a gaban ta tana rarrashin ta ta yarda a kira likita ya duba ta, da k'yar dai ta shawo kanta ta yarda a kira likitan,

aikuwa cikin rawar jiki suka kira shi,  baiwani d'auki dogon lokaci ba yazo, nan da nan ya shiga aikin sa dan ganin yanda jikin ta yayi zafi, allura yayi mata wanda da k'yar ta yarda akayi sannan ya rubuta mata magunguna.

D'aya daga cikin guy's d'in ta ne yaje ya siyo magungunan, tana sha kuwa bacci mai nauyi yayi awon gaba da ita.

***********

_Aliyu Rasheed Ganduje_ ne tare da _Muhammad Hussein D'anbatta_ a cikin _Airport_ sai magana sukeyi k'asa-kasa ta yadda babu mai jiyo su, wayar Muhammad Hussein Aliyu ya k'arba ya saka number Amatullah yayi saving sannan ya ciro wayar sa ya tura wani _video_ a wayar Muhammad d'in sannan yashiga _whatsapp_ yayi ma Amatullah sending sai da ya tabbatar ya tafi sannan ya goge _video_ d'in ya mik'a masa wayar yace _"Muhammad Hussein D'anbatta I know that you can make it perfectly with out any single mistake_"
"so dan Allah kayi min wannan k'ok'arin ka siye min zuciyar ta zanyi farinciki idan _Amatullah Ahmad Fage_ takamu da k'aunar ka wanda zai iya kaita kushewar ta!  Saitayi nisa ta tsunduma sannan ka aikata abinda nace maka ina fata ka fahimta?"
"zakayi amfani da duk wata damar data zo maka,  karkayi fushi karkayi zuciya da dukkan wulakancin dazata yi maka har saita fad'a tarkon sannan ka soma fiddo mata danaka kalolin, hakan bazai samu ba ina k'ara shaida maka harsai kayi hakuri kakai zuciyar ka nesa, ina fatan ka fahimce ni?"

"na fahimce ka Sir insha Allah zanyi kamar yadda ka umurce ni!"

"yauwa!! _the great captain, I salute you on that_ nasan zaka iya! So ya mage takeyi idan zata kama bera?"

"natsuwa takeyi ta k'wantar da kai!"
"hannu ya bashi suka kashe yace a she ka gane mutumina"

"so ina yima fatan alkairi Allah yabaka sa'a sai munyi waya"
Daga haka yasoma hawa matakalar jirgin yanai masa _bye bye_ idanuwan _Muhammad Hussein D'anbatta cike da hawaye yajuya ya tafi bayan yaga tashin jirgin nasu.

*************

Amatullah taji dadin jikin ta sosai, tayi wanka tayi sallah ta shirya cikin wasu k'ananan kaya masu k'yau way'an da suka dace da jikin ta tamkar a tare aka halicce su.

_Dinning table_ ta nufa ta d'an tsakuri abinci kad'an ta d'auko wayar ta ta nufi kujera ta k'wanta ta shiga latse latse a wayar, daga k'arshe ta shiga _whatsapp_ tana ta d'an dube duben ta har zata sauka taci karo da wata bakuwar number wacce ta dauki hankalin ta saboda ganin

_video_ akai mata _sending_ wannan yasa ta shiga tayi saurin bud'ewa dan taga _video_ meye ne?  Lokacin da _video_ d'in yafara nunawa cikin wani irin gigita Amatullah ta mike da ga k'wancan da take bisa kujera ta yi tsaye tana kallon ikon Allah hade da zaro ido tana hawaye zuciyar ta kamar zata fado kasa dan tsananin tsoro da tashin hankali.
_video_ ne kamar a mafarki ita da wani gaye suna _romancing_ juna a gigice tamkar zasu cinye kansu babu ko d'igon kaya a jikin su haihuwar uwar su da uban su bayan sun  koshi da _Romance_ d'in ne suka tsunduma aika ta sabon Allah cikin nuna k'warewa kowanne naso ya nunawa d'an uwan sa shifa k'wararre ne a harkar bayan sungama ya sungume ta ya kaita bandaki sukayi wanka a tare, shima saida suka gama watsewa sannan.
bayan sungama ya d'aukota daga nan _video_ yake karewa,  wani irin ihu Amatullah tasaki tana fadin wayyo Allah na shiga  uku wallahi sharri akai min wallahi banice ba.........

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI* 2️⃣5️⃣to3️⃣0️⃣

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

_wannan page d'in nakune_

_M JABO NUMBARIN NOVEL_

Kuka take sosai tana fad'in na shiga uku ni Amatullah waye yamin wannan mummunar sharrin? Jikin ta sai k'yarma yake zufa kuwa gaba d'aya ya jike rigar ta sharkaf duk kuwa da sanyin da a keyi a garin. Sautin kukan ta ne ya k'aru da ta tuna cewa yanzu wannan _video_ yagama zagaye duniya, wani ihu tasaki tana fad'in no! No! No! Wallahi bani bace! Na rantse da Allah ban aikata ba wallahi sharri akai min wayyyo ni Amatullah sun cuceni sun gama dani.... Da gudu Teena ta shigo a rud'e ta na tambayar ta lafiya meya faru? Wani irin mugun harara ta sakar mata tare da tsawa da gudu Teena ta fice waje tana haki.
Kuka Amatullah taci gaba dayi tana Allah ya isa ga duk wanda yayi mata wannan mummunar k'azafin dan ita sam bata sawa ranta Aliyu bane saboda tasan hakan bai faruba so bata taba zaton zai aikata mata hakan ba.
Lokaci d'aya duk tawani zabge ta fad'a sai kace wacce ta shekara tana ciwo, tamkar wacce aka tsikara ta jawo wayar da sauri ta soma yima number d'in magana kamar haka, _"Mallan menayi maka a rayuwa kanimi ka tozar ta ni ka zubda min mutunci na da martaba ta ta y'a mace!_ Menayi maka?"
"Mena tsare maka?"
"meye had'i na da kai?"
"waye kai?"
"d'an gidan uban waye kai?"
"me kake tak'ama dashi waye uban ka a fad'in Africa da kewayan ta?"
"da kai nake yi waye kai nace!?"
Ta k'arasa rubutun tana hawaye tare da kunar zuci gaba d'aya tarasa make mata dad'i a duniyar nan.

Tsawon minti goma da maganar ta a _whatsapp_ sai ga _reply_ kamar haka, _"Amatullah Ahmad Fage_ kin dad'e kina tsula tsiyar ki muna kallon ki muna k'yale ki bawai dan munajin tsoran ki ba a'a kawai muna d'aga maki k'afa ne saboda matsayin ki na y'a mace mai kima a idon duniya."
"To ashe sam bahaka abin yake ba a gare ki! Domin kuwa ashe kallon kitse mukeyiwa rogo." "Ashe ke d'in tambad'add'a ce an turo ki karatu amman kina ha'intar iyayan ki kina tambadewar ki!" "Dubi irin masha'ar da kike aikatawa a k'asar nan Allah kad'ai yasan yawan mutanan da kike hurd'a dasu, abin takaici Amatullah gaki jahila! Takkwala! Sam bakida ilimi bakida ganewa, amman mai makon ki natsu kisan inda ke maki ciwo a'a sai kawai kika zabi wannan rayuwar kina ganin shine dai dai a gare ki, ga girman kai da wulakanci kin d'aurawa kanki sam bakisan darajar kowa ba! To yanzu dai mun gane dan haka wallahi wallahi mun daina raga maki babu d'aga k'afa duk wanda kikai mawa sai mun wulakanta ki fiye da tunanin ki! Sannan abu na k'arshe da zan gaya maki shine wannan _video_ zai zama sirri daga ni sai ke sai wanda kuka

aikata dashi, amman da sharad'i d'aya idan har kin amince amman fa babu dole dan ni rufa maki asiri kawai nake so inyi, idan kuma kinki wallahi nayi maki alkawarin wannan _video_ tamkar yaje gaban iyayan ki yagama domin suka irin abinda kike aikatawa!  Amman idan har kika yarda da abinda zan gaya maki wallahi nayi maki alkawarin cewa babu mai ji babu mai gani, alkawari ne wannan, kuma ni d'innan ina girmama alkawari sosai."
"sharad'ina bawani mai girma bane soyayyar ki kawai nake da buk'ata, inaso kisoni ki kaunace ni amman kiyi tunani idan kin amince ina jiran reply".

Da sauri ta d'aga wayar ta duba dan jin message ya shigo,  wani irin bakinciki ne ya ziyarci zuciyar ta bacin rai ya lillibe ta a fusace tashiga rubuta masa "lallai na yarda kai matsiyaci ne shiyasa har kake niman soyayya ta ta wannan hanyar, banza kawai d'an matsiya ta aini ka san nafi karfin arzikin ka shiyasa ka biyo ta wannan hanyar to ka sani ni Amatullah nafi karfin ka kai uban kama nafi karfin shi balle kai!  Banza d'an iska, kuma wallahi Allah sai na saka an kulle min kai da zuri'ar ku kaf an jefar da mukullin,  an mance babin rayuwar ku a duniya!  Kasaka kanka cikin tasku da bala'i da masifa wallahi muzuba nida kai saikayi daka sani wawa kawai!"
Gaba d'aya tayi jifa da wayar aikuwa tayi k'watsa-k'watsa, babu alamar zata kuma moruwa.

**********

_Meeting_ gaba d'aya y'an aikin gidan nata suka yi dan gane da yanayin da uwar gidan nasu take ci,  dan kuwa abu yaki ci yaki cinyewa, gaba d'aya ta daina zuwa makaranta,  ta daina walwala,  sam ta canza bata da sukuni, sai rama takeyi kullum a firgice tamkar wacce batada gaskiya abin ya ishe su shine dalilin _meeting_ d'in nasu, sun tsaida shawarar kawai su kira mahaifiyar ta su shaida mata halin da y'ar tata ke ciki dan abin ya fara wuce tunanin su.
Hankali tashe _first Lady  Hajiya Asma'u Ahmad Fage_  tasoma magana cikin tsananin tashin hankali,  "meyasa baku fad'i min ba tuntuni sai yanzu!?"
"meye amfanin ku?"
"gaskiya baku k'yauta minba Bala!"
"adalci kenan kukayi min?"
"d'iyar tawa nacikin irin wannan halin amman akasa sanar dani sai yau!  Masifa taci gaba dayi ta inda take shiga bata nan take fita ba, tamkar zata ari baki, daga k'arshe bayan tagama wanke su tas ta shaida masu zuwan ta nan da kwana biyu kuma kar wanda ya kuskura ya shaida ma Amatullah zuwan ta,  taga haka ta aje wayar zuciyar ta na k'una tana tunanin meyasami y'ar tata haka?".

**************

_NIGERIA_

Wasu had'addun motaci ne guda biyar kirar _venz 360_ masu azabar k'yau, bakake wuluk dasu sai d'aukar ido suke a jere suka shigo cikin _Airport d'in ta MALLAM AMEENU KANO INTERNATIONAL AIRPORT_ waje d'aya sukayi parking a jere,  dogarai ne bila adadin sukai ta

fitowa suka zagaye harabar wajan, kowanne da zabgegiyar dorunar sa a hannu, adai dai lokacin da jirgin ya sauka wani hadaddan gaye yafito daga cikin motar cikin takun sa ta k'asaita ya jingina da motar yana lallatsa hadaddiyar wayar sa ta zamani.

A lokacin da mutanan dake cikin jirgin suka soma saukowa wannan hadaddan gayan ya isa daf da jirgin dai dai lokacin da had'addan gaye mai takama da naira mai ji da kansa d'an k'walisa kuma d'an gayu wanda ya amsa sunan sa wanda y'an mata ke haukar son sa suke kashe makudan kudade gun ganin sun mallake sa kota hanyar asiri ne, watau _Aliyu Rasheed Ganduje_ ya soma tako matattakalar jirgin cikin tsananin isa da takama gaba d'aya yana yin sa ya canza daka kalle sa kasan jinin saurata ne ko k'arya babu a lamarin bare tantama.

Wani irin iska yake shak'a mai dad'in gaske, lallai kowa yabar gida gida yabar shi, wani irin farinciki yake ji daya shaki kamshin k'asar sa ta haihuwa, kuma garin sa wanda yake alfahari da shi, yana alfahari da kasancewar sa cikakken bakano..........

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI* 30to35

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

Da sauri wannan matashin saurayin ya k'arasa gunsa suka rungume juna cike da farin cikin ganin juna.
Murmushi ne k'wance bisa fuskar Ganduje yana cike da tsan-tsan farinciki, _friend_ akwai labarai sosai harsai ka ture, matashin saurayin ya fad'i yana k'ara k'ank'ame Aliyu a jikin sa,
"Allah ko abokina?"
"sosai ma, kaidai muje gida ka huta tukun."
Tafiya suke yi cike da k'asaita suna rik'e da hannun juna kuwanne fuskar sa cike da annuri, a haka suka k'arasa jikin motocin inda dogarai keta zubewa suna k'wasar gaisuwa tare da kirari kala kala irin wanda a keyiwa y'ay'an sarakuna.

A haka motocin ke tafiya a jere gwanin ban sha'awa da birgewa, kai tsaye masarautar kano suka nufa inda tunkafin motocin sugama tsayawa dogarai suka cika ko ina da kiraye kirayen su, murmushin jin dad'i kawai Aliyu keyi.
Har cikin fada dogarai sukai masa rakiya sannan suka juya, cikin sarsarfa ya k'arasa gaban mai martaba inda ya d'ora kansa bisa jikin sa yayinda mai martaba sarki _Abdul Rasheed Ganduje_ ya d'ora hannunsa bisa kan Aliyu yana shafawa dagani kasan yana cike da farinciki mara misaltuwa.
Gaba d'aya fadawan dake tare da mai martaba suka basu waje bayan sun gama kirari sunyiwa yarima d'an sarki barka da isowa.
Cike da girmamawa irin ta y'ay'an sarakai Aliyu ya isar da gaisuwar sa a wajan mai martaba ya amsa masa cike da jin dad'in ganin sa.
"ubana babu sanarwa Saidai kawai muganka haka kamar daga sama?"
murmushi Aliyu yayi yace "Abba ai dama zuwan bazata nayi maku yaron malan kawai na sanarwa zuwa na, shida dogarai suka d'auko ni."
"Abba nayi farinciki dana sameku lafiya, Allah yak'ara maku lafiya da nisan k'wana."
"Ameen Baba na ,ka shiga cikin gida ka huta zuwa anjima".
"to Abba."
Tuni labarin dawowar Yarima ta karad'e ko ina a cikin masarautar, hidima a ka shiga yi ta ko wani bangare, tuni Jakadiya ta k'araso cikin fadar inda ta iske uban gidan nata Yarima na shirin tashi nan ta kwashi gaisuwar ta gun mai martaba kafin tajuyo bangaran Yarima bakin ta yaki rufuwa sai faman kirari take masa inda ta yi masa jagora cikin gida, ko ina suka gifta bayi ne sunata kawo gaisuwa ga Yarima yayin da dogaran da suke take masa baya suke fad'in.
"Yarima ya amsa!".
Kai tsaye d'akin mahaifiyar sa Fulani suka isa shida jakadiya inda jakadiyar ke fad'in,
"Ranki ya dad'e ga Yarima nan ya iso."
Murmushi Fulani tayi tare da gyara kishingidar ta alamar tayi murna da isowar Yarima.
Cikin takunsa mai matukar k'yau da d'aukar hankali ya isa gaban mahaifiyar tasa inda ya zube a jikin ta kamar wani k'aramin yaro yana washe baki, gaba d'aya kuyangin Fulani dasuke faman yidima da ita suka zube suna k'wasar gaisuwa gun Yarima wanda sam hankalinsa gaba d'aya yana kan mahaifiyar sa, Jakadiya ce ta amsa masu tare da bawa Yarima da mahaifiyar sa gu dan su gana,
Gaba d'aya kuyangin suma suka fice dan bawa d'an da mahaifiyar sa gu.

Kallon shi tayi cikin farinciki tace "Yarima zuwa haka babu sanarwa ina fata dai lafiya?"
"lafiya kalau Umma zuwan bazata nayi maku, ai Yaron Mallan ya san da zuwa na."

Wannan matashin saurayin daya taro Aliyu ne yashigo yana fad'in "a'a _friend_ irin wannan nanika haka saikace zaka koma ciki?".
Harare Aliyu ya watsa masa yace "ina ruwan ka sarkin sa ido?"
Dariya ya k'washe dashi yana fad'in "ka taso muje ka huta", kafad'a Aliyu ya make saikace yaro karami, alamar bazashi ba, dariya matashin saurayin wanda ake kira da yaron malan ya k'washe dashi harda rike ciki yace, "iye! Lallai Yarima yau shagwaba ta tashi kenan anga Umma".
Fulani ne ta kalli Aliyu ta ce "Yarima kaje kayi wanka ka ci abinci sai ka kwanta ka huta da yamma sai ka shigo inji matsalar ka dan naga bakin ka akwai magana".
"to Umma yafad'i had'e da mik'ewa tsaye"
Yaron malan yayi masa jagora harzuwa bangaran sa.

***************

_AMERICA_

Amatullah k'wance bisa kujera fuskar ta na kallon sama hawaye sai ambaliya suke bisa k'yakkyawar fuskar tata, tunani take a zuciyar ta har ma maganar ta fito fili bata sani ba, "yanzu ni Amatullah idan su Abba suka ga wannan _video_ yazanyi da raina?"
"  Mezance masu su yarda dani?"
"Dame zan kare kaina?"
"nasani Abba na sallama ni zaiyi, zai cire ni acikin jerin y'ay'an sa"
"wayyyo ni Amatullah nashiga uku sun cuceni sun zalince ni sun gama dani,  bazan taba yafe wa ba!"
Kuka mai karfi tasaki abin gwanin ban tausayi harwani shidewa takeyi.
Tana cikin wannan halin kamar daga sama sukayi ido hudu da mahaifiyar ta _Hajiya Asma'u Ahmad Fage_ wacce shigowar ta kenan a rikice, ganin y'ar tata a wannan halin ne yasata k'ara rikicewa ta nufi isa gunta da sauri.
Cikin tsananin gigicewa
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: Amatullah ta daka wani uban tsalle ta dira daga saman kujerar tayi baya da gudu tana fad'in "wayyo Allah na nashiga uku! Wallahi Allah bani bace mum bani bace wallahi tallahi ban aikata ba sharri akai min wallahi bani bace banyi ba wallahi mum".
Ganin dai uwar ta nufo ta gadan gadan yasata k'wasa da gudu ta fad'a d'aki tana wani irin kuka kamar ranta zai fita tana rantse rantse.

Hankali tashe Hajiya Asma'u ta biyo ta d'akin da sauri ta nufe ta tana fad'in" _wait wait_Amatullah ki natsu kimin bayanin abinda ke faruwa! "

"mum ki yarda dani, na rantse da Allah banyi abu maka mancin hakan ba, wallahi sharri akai min ban aikata ba mum!"

Gaba d'aya uwar ta rikice k'wallah cike a idanuwan ta zuciyar ta tagama karaya, shikenan Amatullah tasami matsalla a k'wakwalwar ta" innalillahi'wa, Inna'ilaihirraju'un!!.

Cikin zafin nama ta rik'o Amatullah dake niman shigewa band'aki, ta girgiza ta da k'arfi tare da daka mata wani mugun tsawa, "Amatullah kalle ni!, Ki natsu ki gaya min meya sameki?"
"meke damunki?"
"waye ya taba min ke? Waye shi waye uban sa a duk fadin k'asar nan!?"
"nayi maki alkawarin kowaye shi sai anyi maki maganin sa indai har ina numfashi a duniya!
Dan haka ki kwantar da hankalin ki ki fad'i min matsalar ki, kinji y'ata?"

A hankali wani irin natsuwa ke saukar mata jikin ta a sanyaye ta bud'e baki da k'yar tace "Mum wani irin mafarki nakeyi dawani _guy_ kusan sati uku kullum sai nayi Mafarkin yabiyo ni da wuk'a zai kashe ni, a cikin mafarkin nawa ne jiya naga na kashe shi da wuk'ar dayake bina dashi".

Ta kare maganar cikin kuka sosai, rungume ta uwar tayi gam gam tana d'an dukan bayan ta alamar rarrashi, "karki damu Amatullah mafarki ne ba gaskiya bane"
"kina addu'a kuwa idan zaki kwanta?"
"inayi Mum inayi kullum".
"to ki kwantar da hankalin ki mafarki ba gaskiya bane kinji?"
Ta gwad'a kai Kawai alamar yarda da zancan uwar.

Da kanta ta had'a ma Amatullah ruwan wanka tayi ta taimaka mata ta shirya cikin wata had'addiyar doguwar riga, da kanta take bata abinci a baki har ta koshi, rabon da Amatullah taci abinci mai yawa haka harta manta.

Kwanan Hajiya Asma'u biyar a k'asar _America_ tana kula da y'arta kafin ta juya _Nigeria_.

*******

A hankali take tafiya cikin shigar ta ta kananan kaya wanda yayi mata kyau sosai kamar a sure a ruga, kai tsaye ta nufi _garden_ d'in da ke bayan gidan rike da sabuwar wayar ta a hannu wanda tacire sim card dinta ta mayar nan.

_Guys_ d'in ta da sauran y'an aikin ta nata kawo gaisuwa amman sam bata kula ko mutum d'aya ba balle ta amsa, haka kawai ta rasa make mata dad'i yau d'innan, kwata kwata bata da _rest of mind_ zaune tayi bisa lallausar koriyar ciyawar dake shimfid'e a wajan, Teena ce ta biyo ta da kayan marmari shak'e a faranti, a gabanta ta aje ta juya.

Kallo d'aya taiwa farantin ta d'auke kai.
Wayar ta ne yashiga kuka, tafi minti biyu tana kallon shi yana kuka yana yankewa ana k'ara kira, d'an guntun tsaki tayi ta d'auka ta kara a kunnin ta,
_"Hello"_

"uhm _sweetheart_ yakike?"
Dif tayi kamar bata jiba dan mamaki ne yacika ta, a hankali ta furta _wrong number_ ta kashe.
Sake kira akayi da sauri ta d'aga da niyyar tayi masifa saidai tunkan ta furta komi taji ance _"Amatullah Ahmad Fage_" har yanzu baki gama tunani bane?"
"yaufa sati d'aya kenan ina sauraran ki".
Gaban tane ya yanke ya fad'i rass!! rass!! cikin rawar baki tace........

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI* 3️⃣5️⃣to4️⃣0️⃣

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

_Wannan page d'in naku ne k'awayan ar'ziki, hakika ina alfahari daku domin kuwa kunzame min jinin jiki na, ina alfahari daku akoda yaushe._

_KHALISAT HAYDAR_
_MAMAN SHAKUR_

_UMMI AYSHA_
_KAUSAR LUV_
_SADIYA LAWAL BALA_
_PHARTYMA ZAHRA_

"Meyasa kake da naci ne?"
"nagaya maka Amatullahi ba matar k'ananan yara bace! Me na sama yaci bare yabawa na k'asa uhm?"
"ko kallon tsoro ka min ne?"
"babu soyayya a tsarin rayuwar Amatullah, auren ma zanyi shi ne dan yazama dole ayi, inaso inyi koyi da fiyayyan alitta, ina sha'awar yara k'ana na, to nasani hakan bazai faruba sai ta hanyar aure, so kaga aure yazama dole indai har inason cikar buri na.
"in yambaye ka mana?"
"uhm ina jinki".

"wanene kai?"
"ina nufin waye uban ka? Meye matsayin sa? Sannan nawa ka tara a duniya? Make gare ka?".
"ina buk'atar k'yakkayawar amsa dan inji ko zan iya maneji da kai albarkacin son da kake kirarin kana min."
"karki damu zakiji komi akai na amman zaifi k'yau mu had'u gani gaki, idona cikin naki abin zaifi bada ma'ana mai k'yau kingane ko"
"uhm! Badamuwa mu had'u a......... Da misalin k'arfe biyar na yamma, saboda inada _lectures_ 2 to 4 kagane ko?"
_"yes ma"_

Washe gari Amatullah cikin shigar ta ta kamala ta nufi makaranta, kanta a k'asa take takun ta tamkar mai tausayin k'asa, wasu littafai ne a hannun ta sai jakar ta dake makale a kafad'ar ta, babu zato babu tsammani sukai karo dashi shima wasu littafan ne a hannunsa, gaba d'aya littafan nata dana shi suka watse a k'asa, a lokaci d'aya suka D'uk'a kowa ya d'ibi nasa, fuskar sa ta leka tana kallon sa kasancewar hular dayasa ta rufe masa fuska.
Wani guntun tsaki taja ta mik'e da sauri tana fad'in "bagidaje! Sai kace bai taba ganin mutum ba, dan tsabagen k'auyan ci yana tafe yana kalle-kalle, tir da k'auyanci da gida danci! Ta watsa masa miyau tayi gaba tana toshe hanci.
Kallo yabi ta da shi yana raya abu a zuciyar sa, wani guntun murmushi yasaki a hankali ya furta, _Amatullahi Ahmad Fage_ kenan! Kinai min kallon biri inai maki na ayaba, a sannu zaki gane hakan, lokaci nazuwa da zaki san waye _Muhammad Hussein D'anbatta_ .
daga k'arshe yabi bayan ta ya shiga ajin shima dan d'aukar darasi.

***********

Masarautar Kano babban masarauta ce mai d'inbin tarihi, mai martaba sarki _Abdul Rasheed Ganduje_ shine ya kasance mahaifi a gun _Aliyu Rasheed Ganduje_y'ay'an mai martaba guda goma sha biyu ne, inda suka kasance mata guda goma sha d'aya, zuwan amaryar sa Fulani d'iyar mai martaba sarkin katsina watau _Halimatus Sadiya_ shine ta haifa masa Yarima Aliyu, wanda mai martaba ya d'auki son duniya ya d'aurawa wannan d'a nasa kasancewar sa namiji guda d'aya tilo.
Yarima Aliyu ya tashi cikin soyayyar y'an uwa kowa na sonsa, Aliyu yaro ne mai farinjini da k'warjini a ckin jama'a, ga jarumta da juriya, Aliyu yakasance miskilin mutum na k'arshe, sam baya murmushi bare azo ga dariya, kafin Kaga murmushin Aliyu sai ka taki babban sa'a.
Aliyu mutum ne mai kirkin gaske da dad'in zama idan ka fahimce shi, yana da tsabta mai ban mamaki, gashi k'yakkyawa na nunawa a sa'a,  gaba d'aya karatun sa tundaga kan _secondary school_ har gaba da ita har Master's d'in sa duka a _America_ yayi shi inda yagama yanimi _lecturing_ a nan _Catholic University of America_ Aliyu baya da burin daya wuce yazama _lecturer_ shiyasa daya samu ya rike aikin sa da mahimmanci sam baya wasa dashi, sam mai martaba bai hana saba dan kuwa yasan burin Aliyu kenan tun yana yaro.
Rana d'aya Amatullah tazo ta rushe komi, wannan dalilin yasa shi d'aukar tsanar duniya ya d'ora shi akanta, yasha alwashin sai ya wargaza farincikin ta yanda ta wargaza nasa.

******

_Muhammad Hussein D'anbatta_ ne zaune yana jiran isowar Amatullah, izuwa yanzu yagama k'agara da zuwan nata, shikam sam baya son mutum mai saba alk'awari dan shi yana aiki da lokaci ne, wannan dalili ne yasa ran sa ya d'an sosu, agogon hannun sa yake kallo a zuciyar sa kuwa fad'i yake "d'an _Nigeria_ kenan komi sai yayi _African time_  wayar sace tashiga k'ara inda ya d'auka ya kara a kunnin sa yana jira yaji mezata ce masa,
" bangan kaba "
"ina nan inda kika ce in zauna ki k'araso zaki ganni ya kashe wayar sa.
A hankali ta k'araso cikin takun ta ta tak'ama da isa, bayan sa kawai take iya hango wa nan danan zuciyar ta ta tsinke, kujera taja ta zauna suna fuskan tar juna, lokaci d'aya duk wata gaba ta jikin ta ta tsaya cak da aiki, wani irin bak'in ciki da takaici ya lullube ta, tamkar zata shak'e shi ta mik'e tana nunasa da yatsa "kaiiii ni tsarar ka ce da zakayi wasa da hankali na?"
"Amman lallai kacika mara mutunci,"
"to waima in tambaye ka?"
"shin aiko ka akai waje na ko kuwa kai d'in ne ka kawo kan ka da kanka guna dan maula!?"
"to bari kaji idan aiko ka akayi ka koma ka gayawa uban gidan ka ni _Amatullah Ahmad Fage_ nafi k'arfin sa nafi k'arfin uban daya haife shi."
"Idan kuma kai d'in ne ka kawo kanka dan tsabagen rashin kunya da rashin d'a a to ka bud'e kunnuwan ka kaji ni da k'yau."
Tayi wani irin juyi a gaban sa tace "kalle ni da k'yau ka k'are min kallo, ko ba a gaya maka ba

kasan cewa nafi k'arfin gaba d'aya zuri'ar ku, to dan me zaka rainawa kanka wayau ka ha'inci kanka da kanka?"
"Zanmaka gargad'i da babban murya, ka kiyaye ni ka rufa wa kan ka asiri kasamu ka gama karatun ka lafiya idan baso kake kayi asarar _scholarship_ d'in ka bane, wallahi idan ba ka kiyaye ni ka fita harka taba sainayi sanadiyyar barinka makarantar nan kaji na rantse maka, kuma _video_ dakake min barazana dashi nice d'in ai ka gani ganin idon ka, na isa ne shiyasa na aikata hakan, kai idan ka isa kayi hakan mana, idan ka ga dama ka turawa duka y'an duniya kace ga _Amatullahi Ahmad Fage_ na fasikanci! .
Kanka kayiwa bani ba dan kunyar mara kunya asara ce, idan kuma iyayena kake tak'amar su gani to su gani d'in sai me zai faru?"
"Babu abinda zai faru illa iyaka susani cewa d'iyar taso ta k'osa aure take so!"
"dan haka kayi gudu kaje ka fad'a masu kokuma inbaka _number Mr President_ d'in ne?" tayi tambayar cike da rainin wayau tana kallon cikin idon sa.

Tsananin mamaki yasa _Muhammad Hussein D'anbatta_ kasa cewa komi illa binta da ido da yakeyi, ta watsa masa harara ta wuce abin ta ta barshi nan zaune yana mamaki.
Wayar sa ya ciro yakira Aliyu ya shaida masa yanda sukayi, murmushin takaici Aliyu yayi yace "ka k'yale ta kawai ka fita hanyar ta zansan yarda zamu bullo mata, intaki hagu ai bata ki dama ba!.

******

Su Amatullah sun k'are jarabawar su lafiya inda da sun dawo hutu zasu shiga shekarar k'arshe a karatun su, sai dai abin takaici shine gaba d'aya jarabawar data wuce wacce sukayi Amatullah bata aikata abin kirki ba duk ta fad'i yawancin _courses_ d'in dan haka gamawa _next year_ bada ita ba, aikuwa shugaban makarantar da kansa yakira mahaifin ta ya gaya masa abin da ake ciki, godiya kawai _Mr President_ yai masa tare da tambayar sa koyasan abin da ke d'aukewa d'iyar tasa hankali, kunsan bature shi bai wani iya saya magana ba kai tsaye ya shaida masa cewa kila kan d'iyar tasa ba na d'aukar karatu bane shiyasa kullum take fad'uwa jarabawa, amman shawarar dazai basa me zai hana ta dawo gida tayi karatun a gaban sa kila za a dace, godiya _Mr President_ yayi masa sosai sukayi sallama cike da mutunta juna.
Bayan k'wana biyu da gama jarabawar su Amatullah ta ta tattaro ta dawo gida _Nigeria_ ..........

_Tofa yanzu ne zamu shiga cikin labarin tsundun!_.

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*

[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI* 40to45

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

"Yaron Malan da gaske nake aure nake so a nima min kacire maganar wasa dan haka na wakiltaka kaje ka sanar da Fulani sak'o na."

Mamaki shimfid'e a fuskar Yaron Malan yake kallon Aliyu, wai yau Aliyu da bakin sa yake furta yana son aure, Aliyu da ya tsani ai masa maganar aure harma iyayan nasa sun gaji sun zaba masa mata, idan bai manta ba sati uku kenan da mai martaba yai tattaki har gidan gomna shida mutanan sa suka nimowa Yarima Aliyu auran d'iyar gomnan wanda har anbasa ankuma saka rana, dama mai martaba yace idan lokaci yayi za a d'aura auran akai masa matar sa can k'asar idan bai zoba,

sai gashi yanzu da kansa yake masa wannan zancan, wannan shine *RUGUNTSUMI* _(NA HAUWA JABO DA FIDDAUSI SODANGI)_

"Malan idan bazaka iya zuwa ba in tura Jakadiya! Naga ka tsare ni da ido kamar baka taba gani na ba."

"Yarima bawai bazani bani amman gaskiya akwai matsala!"

"matsala? Allah ya raba mu da ita Yaron Malan".

Yarima da gaske nake fa, nan dai cikin k'wantar da murya ya shiga zaiya no masa abinda ya faru.

Murmushi Aliyu yayi yace "Alhamdulillah Allah abin godiya! Gaskiya nayi farinciki da jin wannan zance naka abokina, ya k'arayin murmushi tare da fad'in fad'uwa tazo dai dai da zama!".

Da mamaki Yaron Malan ke duban sa da k'yar ya iya fad'in "Yarima dama itace kake so a nima maka auran tane?  Kafa san y'an matan biyu ne, Ya da k'anwa,  ance anriga anyiwa yayan miji shine aka baka k'anwar dan bama ta gama karatu ba shekarar k'arshe take".
Kafad'ar Yaron Malan Aliyu ya dafa yace "karka damu mutumina nasan abin da nake yi, kaje ka gayawa Fulani sak'o na kawai,"
ya wuce abin sa yabar Yaron Malan sake da baki tare da binsa da kallon mamaki yana al'ajabin hali irin na Yarima.

*****

"Shi Yariman ne ya turo ka da wannan maganar?"
Kan shi a k'asa yace "nayi masa bayanin abinda ke faruwa Fulani amman Yarima ya dage sai nazo na gaya maku amman kuma abin mamaki shine Yarima yayi murna da zancan auran da aka nima masa, to a nawa tunanin dai mata biyu yake so yayi da dukkan alama."

Murmushi Fulani tayi tace "hoo Yarima rigima, inban da rigima irin ta sa ina shi ina mata biyu a yanzu?"
"Fulani kusawa abin albarka kawai, ina ganin babu abinda zai gagari Yarima da yardar Allah!".
"to shikenan Yaron Malan zan yiwa mahaifin sa magana muji ta bakin nasa insha Allahu".
"to Fulani Allah yasa a dace Yarima na godiya."

********

Cike da farinciki Mai martaba ke duban Fulani, "a ina ne za a nima masa auran ne?"
"d'iyar waye?"

"A'a nima bamuyi maganar da shi ba, Yaron Malan ne yazo min da zansan."
Jakadiyya mai martaba yasa akai masa kiran ta ya dube ta yace "Jakadiyya kunyi wata magana da Yarima ne akan batun niman auran sa?"
"eh ya shaida min cewa sun k'ulla alakar soyayya shida y'ar gidan shugaban k'asa,  yace yana so a nima masa auran ta insan samu ne ma a yi bikin lokaci d'aya da wanda kuka nima masa."

Murmushi mai martaba yayi yace "Yarima kenan, shi nan har zai iya rike mata biyu a shiririta irin nasa?"
"ban tari numfashin kaba ranka ya dade Allah yaja da zamanin ka, Allah ya huci zuciyar mai martaba sarki, ina ganin yakama ta animawa Yarima auran yarinyar nan, saboda yayi mana biyayya ya amshi zabin mu batare da nuna bacin rai ba, mun dade muna matsawa Yarima akan ya fiddo matar aure yak'i, to sai gashi yanzu da kansa yace ga wacce yake so, ina ganin bai dace mu yi biris da zancan nasa ba, Yarima yaro ne mai ladabi da biyayya, bai taba ketarewa umurnin muba, dan haka ina rok'on mai girma sarki dayayi duba ga maganar Yarima a amsa mashi but'atar sa Yarima yana bawa sarki hakuri idan har maganar sa ta bata zuciyar mai

martaba."

"shikenan Jakadiya Allah yayi mana jagora ya shige mana gaba."
Gaba d'aya suka amsa da Ameen.

********

"kimin shuru Asma'u so nawa zangaya maku cewa bana son yawon da yarinyar nan take yi! Yanzu k'arfe nawa?"
Tunda yarinyar nan ta dawo kullum ba ta da aikin yi daya wuce yawo! Sannan na hana ta fita ita d'aya amman bataji, yanzu lokacin siyasa ne komi na iya faruwa Asma'u meyasa ba kwa nima min kwanciyar hankali ne kullum keda d'iyar ki!?"
Na tabbar yawon gantalin ta take tafiya acan ba karatun take ba shiyasa kullum bata da aiki saina fad'i jarabawa, amman komi yazo k'arshe insha Allahu, ku shirya gobe mai martaba sarkin kano zai zo shida mutanan sa domun niman auran ta kuma nariga na yanke hukuncin basu, dan haka zan amshi sadakin su a goben asa rana in kaudata kozan sami k'wanciyar hankali, nagaji da tijarar yarinyar nan!".

Jiki a sanyaye _first Lady_ Hajiya Asma'u ke kallon sa kafin ta bud'e baki da niyyar yin magana ya dakatar da ita ta hanyar d'aga mata hannunsa, "nariga nagama magana Asma'u bana son jin komi!"
Suna a haka gimbiyar ta shigo da sallama d'auke a bakin ta, bata sami ikon k'arasawa ba sakamakon had'a ido dasukayi da mahaifin nata, wani irin tsawa ya daka mata yana fad'in daga ina kike?
A tsorace ta kalli mahaifiyar ta jikin ta na rawa, kauda kai uwar tayi taga k'arshe tama haye sama ta barsu nan,
"badake nake ba daga ina kike nace?"
Bakin ta na rawa tace "Abbba _ice cream_ naje shaaa... Wani mugun tsawa ya daga mata tare da mugun kallo, baya tayi da sauri tana kallon sa kamar ta zura da gudu take ji.

"Shan _ice cream_ da daddaran nan?"
" Amatullah bakida hankali ne?"
"k'arya kikeyi ba abinda yakai ki fita kenan ba! Kigaya min inda kikaje kafin in tattakaki!."

"Abba bikin k'awata naje kuma na gayawa _mum_ ........"

*DEDICATED TO*

*KUBRA USMAN BALA*
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI* 45to50

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

_Wannan page d'in naki ne my sweet sister (Maman Rabi'a) Sodangi tana son ki tana k'aunar ki tana kuma alfahari dake a koda yaushe._

Wani irin mugun kallo yake watsa mata kafin yafara fad'a cikin kakkausar murya,
"Amatullah meyasa baki gudun zuciya ta?"
"Sau nawa zan gaya maki bana k'aunar yawon dakike yi?"
"meyasa ni ban isa in gaya magana kiji ba iye!!?"
"watau kin d'auke ni mutumin banza ko, ga k'annanki nan suna tasowa duk abinda suka ga kinayi suma shi zasuyi dan haka ki maida hankali kici gaba kada ki fasa kinji Allah yaba da sa'a.
Ya wuce yabar ta nan tsaye jiki a sanyaye.

Duk sai taji babu dad'i zuciyar ta kamar zai fad'o k'asa dan harbawa.
Cikin sanyin jiki ta haye sama kai tsaye d'akin mahaifiyar ta nufa, tasan tayi laifi dan haka ta

soma rabe-rabe, tsawa ta daka mata tace "haka mukai dake ko?"
"yanzu k'arfe nawa?"
"dak'yar ta iya bud'e baki tace _"am sorry mum_ wallahi bansan dare yayi sosai haka ba.
_"shut up!! Stupid girl!! Get out of my room_ kafin in taso in k'wad'e ki kinjawo min fad'an shi hankalin ki ya kwanta."
"ki fita nace!".

Jikin ta a sanyaye ta fito daga d'akin ta nufi nata.
Tana saka k'afa a cikin d'akin wayar hannun ta yasoma kuka, ganin bakuwar _number_ yasa taki d'auka harya katse.
katsewar wayar ne yasa ta ajiye shi gaban Madubinta hawaye na ci gaba da bin kuncinta, _bathroom_ ta nufa don ana ta kiraye kirayen sallar isha'i ne gashi ko Magrib bata yi ba.

Ta dad'e zaune kan darduma bayan ta idar da sallar, daga bisanni ta mik'e da k'yar ta fita zuwa _kitchen_ don yunwa take ji, tukunyar dake kan gas ta bude taga miyar _Vegetable_ din da _first Lady_ tayiwa Abban ta na dare, dan shi baya cin girkin kowa in bana matar saba, shiyasa duk tafiye tafiyan dazai yi da matar sa yake tafiya.

yatsine fuska ta yi ta rufe tukunyar a hankali kamar tana tsoron kar a gane ta bude, indomie guda daya ta dauko cikin _store_ duk da ba shi bane a ranta, kawai dai bata jin yin girki ne kuma bata jin zata iya kiran wani d'an aiki dan yai mata girki yanzu.
ta ciro kwai biyu da zata dafa, cikin minti goma ta gama hada Indominta ta dauka ta fita zuwa dakinta, gaban Madubinta ta ajiye indomie d'in ta shiga _bathroom_ don yin wanka,
Ta riga ta saba ba ta iya cin abinci da zafi sai ya huce, shiya sa ta shiga wankan ta don ya huce kan ta fito.
tana fitowa daga wanka ta d'an shafa mai ta feshe jikin ta da turaruka masu k'amshin dad'i, sannan tasa kayan baccin ta.
_TV_ ta kunna ta sa _series_ d'in da take kallo, sai kusan k'arfe sha d'aya ta kashe kayan kallon don ta gaji, sannan ta mik'e ta nufi indominta dake gaban Madubi har lokacin, bata damu da sandarewar da yayi ba ta d'auka zata bar wajen wayarta ya shiga _vibrate_, ta k'ura ma _screen_ d'in wayar ido sannan ta d'aga a sanyaye, ta kara a kunne,
sallama yayi mata cikin tsadaddan muryar sa, can k'asa, ta amsa sannan tace "waye ne?"
gyada kai yayi kamar tana ganin sa yace “mutum ne mai daraja"
tayi shiru kamar ruwa ya cita tana tunanin inda ta san muryar, shima shurun yayi bayan kamar minti biyu yace _"Amatullah Ahmad Fage_"
"Ashe abinda ya faru da ke kenan?"
Tsabagen dakikanci da jahilci yasa baki ci jarabawa ko d'aya ba! Kai!! Gaskiya kinyi asara wallahi anyi asarar kud'in tara.
Yaja wani ajiyar zuciya sannan yayi murmushi mai fidda sauti wanda saida taji shi har ranta,
yace "bama dai wannan ba ina fata dai kina cin abinci sosai danni kinsan bana son mace y'ar sololuwa kamar a hure ta fad'i dan haka ki dage da cin abinci gaskiya, dan kinsan ni jarumi ne a wannan fannin shiyasa bana son mace lange lange karta karye.

Murmushin mugun ta yakuma yi kafin a hankali kamar mai tsoron magana yace, _"nyc nyt rest, u pray b4 goin to bed"_ ya katse kiran,
Sororo tayi rike da wayar a hannu ko shakka babu wannan _Aliyu Rasheed Ganduje ne_ to me kala mansa suke nufi?
Lallai Aliyu na niman ta da rigima, yazama dole ta gyara masa zama.
kasa cin indomin tayi, ta nemi yunwar da take ji ta rasa, ta kalli agogo sha d'aya da rabi, ta bude k'ofar d'akinta a hankali rike da plate din indomin ta nufi _kitchen_ta bude k"ofar bck yard ta zubar cikin waste bin sannan ta rufo k'ofar ta dawo cikin _kitchen_ta wanke _plate_ din ta ajiye, ta dauki _cup_ ta hada _tea_ ta koma d'akinta, a bakin k'ofa suka had'u da mahaifiyar tata zata sauka k'asa harara ta watsa mata da sauri Amatullah ta d'auke kanta ta shige d'aki zuciyar ta babu dad'i ta tsani fushin iyayan nata.

A hankali take kurban _tea_ d'in ta tana tuna kalaman Aliyu nan da nan zuciyar ta tashiga k'una, gaskiya idan ban maida ma Aliyu martani ba ya cuce ni! Da sauri ta jawo wayar tashiga rubuta masa _messsge_ kamar haka:

_"Kanada asara ne dan na fad'i jarabawa? Kokuwa uban kane ke biya min kud'in makarantar? Banza d'an iska kawai uban y'an shishigi ba a damu da shiba sai kutsa kai yake babu k'warjini!_.

Ta tura masa ta kashe wayar ta gaba d'aya ta k'wanta bayan tayi addu'ar k'wanciya.

Da safe sai k'arfe sha biyu da rabi sannan ta sauko k'asa, bayan tayi wanka ta shirya cikin wata y'ar karamar dogowar riga wacce da kadan ta wuce guiwa ta sauka k'asa nan ta tadda ma'aikata cike sai hidima sukeyi da alamar dai yau bak'i za ai a gidan nasu duk da basu rabo da baki amman da dukkan alamu na yau sunsha banban da na kullum.
Kad'an ta d'an tsakuri abincin ta tashi ta nufi d'akin mahaifiyar Murmushi tasaki ganin yanda uwar tayi masaifar k'yau kamar zata wani gasan k'yau.

_"wow!! You look so cute Mum!"_
"Allah ya barmin ke _my sweet mother_"

Murmushi uwar ma ta sakar mata tare da fad'in _thank you sweetheart_ da alamar harta huce dai, da gudu Amatullah ta k'araso ta rungume ta tana murna tare da sakar mata sunba a kumatu.

_"daughter_ ga kaya nan ki d'auka kije kisake wanka kisaka su kiyi k'walliya tamkar za a kai ki d'akin miji, in nace k'walliya ina nufin kiyi k'walliya wanda ni kaina zan kasa gane ki kingane ko?"

"mum yanzu fa nayi wanka kuma ina ma zamu haka mum ko bak'i Abba zai yi ne?"
"banason surutu Amatullah kiyi abinda nace kawai".

A sanyaye ta isa jikin gadon ta sa hannu ta sunkuci d'an akwatin da kayan ke ciki ta fice a d'akin kamar wacce k'wai ya fashewa a ciki..........

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI* 5️⃣0️⃣to5️⃣5️⃣

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

*ARASHI!*

_k'irk'ira, tun ma ta labari irin na zube ba, aba ce wacce ta ke k'ulluwa da zururruka ma su kishiyan juna, ta fuskar halaiya da d'abi'u, wad'anda suka sha banban daga wannan mutum zuwa ga wancan mutum, daga wancan gida zuwa ga wancan gida, daga wannan gari zuwa wancan gari, daga wannan kabila zuwa ga wancan kabila, daga wannan Al'umma zuwa wancan Al'umma._

_Don haka wanda wani hali a cikin wannan labari yayi kaman ce danata to arashi ne aka samu, kamar yanda na cikin labarin bazai ce wani mutum dayake a wajan labarin ya daukar masa hali ba, to shima wanda yake a waje kada yace an aikata halin sa, haka kuma kamar yanda kowani dan adam yake tauyaiye ba cikakkeba, Allah shi kadai ya kebanta da siffar cika, don haka labari ma zai iya zama dai dai da ra ayin mai karatu kuma zai iya zama akasin haka, idan aka sami dayan biyun wayan nan to badaga marubuciyar bane daga wayanda abin ya shafa ne acikin labarin, .idan an tashi suka wanda abin ya shafa za a soka ba marubuciya ba, nayi wannan maganar ne da masu cece kucen cewa bai dace aiwa Amatullah kishiya ba, ina so kusani cewa kowani mutum da tasa kaddarar, kuma kishiya ba aibu bace ba dan haka a kiyaye,

Sodangi tana maku fatan alkairi_.

Wani wankan ta sake yi kamar yadda uwar ta umurce ta dayi, tana fitowa ta zauna gaban madubi ta tsantsara kwalliya nagani na fad'i tayi azabar k'yau tamkar a sace ta a ruga.

Akwatin ta bud'e ta sanya d'an kunni da abun wuya da d'an hannu na zinari mai bala'in k'yau sannan ta ciro riga da zani na less d'in dake cikin akwatin ta sanya rigar ta soma kici-kicin d'aura zani saidai sam takasa d'aurawa, a haka ta rik'e zanin a hannu ta fita zuwa d'akin mahaifiyar tana tura baki gaba.

Ido uwar ta tsura mata tun shigowar ta dan ganin irin k'yaun data yi,

"mum wannan zanin yaki d'auruwa nayi nayi na kasa, mum kinsan fa ni bana son zani dan ban iya d'aura shiba sai yai ta son yada mutum k'asa, nidai gashi ki taya ni d'aurawa, ta k'arasa maganar tamkar zata fashe da kuka.

Zanin uwar ta k'arba a hannun ta tace ta bud'e k'afa sosai ta d'aura mata ya zauna tsaf kuwa kasancewar Amatullah tubarkalla akwai k'ugu,

D'an k'walin ta kuma amsa ta d'aura mata shi tamkar an nad'a goggoro, nan da nan Amatullah tayi kyau na d'aukar hankali, abin ba a cewa komi, tayi kyau iya kyau.

_"Wow daughter kinyi kyau sosai you look so cute_"

_"thank you mum_"

"mum wai suwaye zasu zo ne?"

"kiyi shuru da bakin ki zaki gani"

************

Da misalin k'arfe biyu da rabi na rana mai martaba sarkin kano da tawagar sa suka iso vila k'arba ta mutunci akai masu tare da karrama su, mai martaba yayi matukar farinciki da irin tarbar da akai masu, liyafa sosai aka had'a masu,bayan sunci sun sha nan suka gabatar da abin da ya kawo su, inda atake _Mr President_ ya basu d'iyar tasa inda ya amshi sadaki naira dubu d'ari acewar sa mafi k'arancin sadaki yafi albarka.

Nan aka tsaida rana nan da wata uku mai zuwa idan Allah ya kaimu, anan mai martaba ya shaida masa auran daya nimawa Yarima, inda sam _Mr President_ bai nuna damuwar saba illa farincikin daya taya su tare dasawa abin albarka, a zuciyar sa kuwa yana jinjina gata irin na yarima.

_Mr President_ yai kiran _first Lady_ tazo ta k'washi gaisuwa gun mai martaba inda yai mata kyautar makudan kudade.

Sun dade suna tattauna matsalolin da ya shafi al'umma daga k'arshe suka gano inda matsalar take nan _Mr President_ yace insha Allahu za a duba a gani domin akawo k'arshan abin da izinin Allah.

Mai Martaba yasa akira masa surukar tasa Amatullah domin kuwa yana jin k'aunar ta har a zuciyar sa, abinda Yarima Aliyu keso ai dole ne yataya shi son sa.

K'ara gyara Amatullah mahaifiyar ta tayi inda ta raka ta har kofar palon da bakin ke ciki inda ta k'ara jaddada mata ki kama kanki banda kallon mutane tsage tsage ki nuna kunya sosai sarkin kano ne da mutanan sa.

Tana shiga palon bakin ta d'auke da sallama kanta a k'asa dogarai suka soma yi mata kirari, "barka da shigowa Gimbiya, sannu y'ar Toron giwa. Alherin Allah ya kai maki y'ar farin jini, Tauraruwa sha haske, Hasken ki baya k'arewa matukar kina tare da wata, Y'ar shugaban k'asan matar d'an sarki kuma Sarki mai jiran gado, Allah ya kashe makiyan ki ya bar mana ke ya nuna mana ranar auran ki da yarima, mace d'aya tamkar da goma, Alkyabbar mata".

Wani irin gingirin gin Amatullah taji, nan da nan taji kanta yayi k'ato duk da kalaman nasu sun d'aure mata kai matuk'a, k'asa ta zube ta k'washe gaisuwa gun mai martaba, kafin ta gaida sauran mutanan, nan dogarawa suma sukai ta kawo nasu gaisuwar gun ta, nan mai martaba ya dafa kanta cike da farin ciki yata saka mata albarka, yayi mata addu'oe sosai sannan daga k'arshe yasa aka mik'o masa wani had'addan k'wando mai ado sosai da kansa ya bude ya ciro wani had'addan alkyabba yasa ka mata, nan da nan ta haska gurin gaba d'aya, ya ciro damin k'udin ya bata amman sam taki karba babu yanda baiyi ba, bata karba ba, hakan ba karamin burge mai martaba yayi ba.

Saida mahaifin ta yasa baki sannan ta yarda ta karba, nan ta yi masu sallama ta mike da k'yar ta bar palon, mahaifiyar tata ce ta tare ta tana fadin _"Wow my sweetheart_ kinga yanda kikayi kyau kuwa?"

_"so tell me what happened there?"_

Nan Amatullah ta shiga zaiyano mata komi babu abinda ta boye mata, jindadi shimfide a fuskar uwar, ta nuna tsananin farincikin ta, nan ta sanar da Amatullah abinda ke faruwa,
Wani irin ihun murna Amatullah tayi tare da tsalle, tana fadin, "masha Allah, Allah na gode maka".
ta fashe da wani irin dariya tana fadin, "lallai za ayi ta! Amatullah a masarautar kano! _Wow_ lallai zanyi wulakanci son raina! Intaka uban da nake so inyi iko inyi takama son raina!"

Takara fashewa da dariya, tace "Aliyu! Yazamar min dole innimoka a fadin kano in nuna maka iyakar ka."
"Aliyu wallahi Allah saina muzan taka na wulakanta rayuwar ka! Dole in koya maka darasi, in nuna maka cewa bakin rijiya ba wajan wasan yaro bane."
"Aliyu! Aliyu! Aliyu! _you will pay for it._"

Sororo uwar ke kallon ta, kafin tace ke ki kama kanki fa duk wani mugun hali dawani rawar kai dole ki aje shi gefe da yanzu ba da bane! Kinji na gaya maki.

Bayan mai martaba da mutanan sa sun gabatar da sallar la'asar suka d'auki hanyar komawa kano daga abuja.............

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*

[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI* 55to60

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

_Afuwan y'an hidimomi ne suka saka ni gaba shiyasa kuka jini shuru k'wana biyu._

Bayan k'wana biyu mai martaba yayi ma Yarima umurni daya je _government house_ shida Yaron Malan domin yagana da Amaryar sa, ba a son ran Yarima ba ya shirya shida Yaron Malan suka nufi _government house_ d'in Yaron Malan sai zolayar sa yake, "iyyee!! Yarima d'angata mai mata biyu, Allah yasamu a danshin ku.

A fusace Yarima ya dube shi yace "dallah Malan ka sarara min nima ba a son raina ba dan duka babu zabi na a cikin su kawai dai kaddara ce ta hau kaina amman ina Aliyu ina mata biyu! "

Cike da mamaki Yaron Malan ke duban sa, dak'yar ya iya bud'e bakin sa yasoma yiwa Yarima tambaya, "bangane babu zabin ka ba a cikin su harda Amatullah d'in da ka rikicewa mutane a kanta?"

Guntun tsaki Yarima yaja kafin yace "Amatullah zan aure ta ne kawai saboda d'aukar fansa!, Zan auri Amatullah ne saboda in nuna mata cewa ni Aliyu Haydar ba tsaran ta bane, in nuna mata cewa tabbas akwai banbanci tsakanin mace da namiji, in nuna Mata cewa abin da namiji zai iya mace bazata taba iya k'watan kwacin shiba.

Amatullah ta raina ni raini na k'arshe so ina so mu goge raini ni da ita ta gane waye babba a tsakanin mu."

" Ita kuma wannan yarinyar da bansan sunan taba zan aure ta ne saboda biyayya wa mai martaba, zan koma k'yautata mata in zauna da ita saboda Allah albarkacin mahaifina."

Ajiyar zuciya Yaron Malan yayi yace "hooo!! Yarima sarkin rigima, to me ita Amatullah d'in tayi maka ne haka? Kokuma in ce mai kayi mata har ta raina ka haka, kukeyiwa junan ku irin wannan kiyayya haka mai zafi?"
"Hmmmm!!!! Bazaka gane ba, ka k'yale ni da yarinyar nan kawai!."
"Hmmmm Yarima kenan, nidai shawarar dazan baka shine kabi a hankali, saboda nariga nasan ka na san halin ka, duk abinda ka tsana tsana mai tsanani to tabbas wata rana zaka soshi so kuma mai zafin gaske, dan haka kabi a hankali kaji na gaya maka."

Wani wawan tsaki Yarima yaja ya d'akawa Yaron Malan duka a cinyar sa dan shi ke tukin yace "Allah ya tsare ni, bakin ka ya sari danyan kashi, wallahi bakada mutunci Yaron Malan ni kakeyiwa wannan fatan?"
"gaskiya na fad'i Yarima ka yarda ko kada ka yarda haka kake.
Suna cikin wannan gardamar suka isa _government house_ an riga ansan da zuwan su dan haka har cikin a ka shigar dasu, a babban, palo akai masu masauki inda y'an aikin gidan suka cika masu tebur da kayan mak'ulashe fannin abinci da kayan marmari, sai laimuka masu sanyi, Yarima yaji dad'in yanda aka tarbe su da mutunci, ruwa kawai ya d'an kurba, Yaron Malan ne yad'an sha _fruits_ d'in shima ba da yawa ba, sun zauna na kusan minti sha biyar har Aliyu yasoma hassala sai ga mai girma gomna ya shigo palon da sallama, cikin fara'a yace "A'a yau Yarima ne da kanshi a gidan namu?"
Cikin jin kunya Aliyu ya sauko da ga kan kujerar shima Yaron Malan ya sauko suka gaida shi cikin girmamawa, fuskar sa a sake ya amsa da yake mutun ne shi mai raha nan yaita jansu da hira daga k'arshe yai masu nasiha mai ratsa Jiki ya mik'e yace bari ya turo masu Amaryar tasu, ya fad'i cikin tsokala, godiya sukai mashi sosai cikin jin dad'in.
Bayan minti kamar goma suna ta d'an hirar su sama-sama k'amshin turaran tane yasoma sanar dasu isowar ta kafin suka jiyo takun ta k'was k'was k'was, shuru sukayi suna jiran shigowar ta, gaba d'ayan su fuskar su na kallon k'ofar dan suga Amaryar tasu ma'abociyar kamshi da tsafta, dan da alamu zatai tsafta a cewar Aliyu a zuciyar sa, dan kuwa shi yana girmama kamshi.

Shigowar ta had'e da sallamar ta shi yayi sanadiyyar tashin Aliyu Haydar a zabure tamkar wanda aka tsikara da allaura, idanuwan sa a kanta itama haka, kallon kallo sukeyi wa juna tsawon lokaci, wani irin farinciki had'e da mamaki mai tsanani yakama ta, tarasa a wani irin hali take ciki, wai yau ita ce da _Aliyu Rasheed Ganduje_ matsayin wayan da zasu auri juna ikon Allah sai kallo, wani zuciyar ne ya kwabe ta da fadin "uban wa yace maki Aliyu ne angon? Baki ganin su biyu ne? Kika sani ko d'ayan ne angon naki?"
Aliyu ne ya katse ta da fad'in _"KHADIJA MUHAMMAD DALA!_"
"kece Amaryar tawa dama?"

Cikin wani irin murya mai cike da farin ciki yayi mata tambayar, sam yakasa boye farin cikin sa.
Hannun ta ya kama ya zaunar da ita akan kujerar da ke fuskan tar tasa, ya dubi Yaron Malan yace "kaga yar k'yakkyawar Amarya ta a shema na santa student d'ita ce kuma aminiyar _Amatullah Ahmad Fage_ ka ga ni wannan abu yaiwa dadi matuka, Allah ya k'arawa mai martaba nisan kwana, gaskiya bansan irin farincikin dana ke ciki ba yau!."
Yaron Malan ya galla masa harara yana fad'in "adai juri zuwa rafi....."
Katse shi Yarima yayi "dalla Malan kar ka cika min ita da surutu!".

Guntun tsaki Yaron Malan yayi yace "kiyi hakuri fa da halin wannan rigimammen mijin naki, yacika rigima kamar wani kankanin yaro!."
Murmushin yak'e Khadija tayi tace "uhmm ai ni nasan yaya Ali na bashi da rigima sam mutum ne shi mai gaskiya a koda yaushe, so fad'in gaskiya ai bazai taba zama rigima ba!"
Ta kare maganar tata tana Murmushi tare da kallon fuskar Aliyu wanda shi kansa ita yake kallo.
"iyyeee!!!! Lallai Khadija ashe kema ba k'yalle bace! Watau kina bayan mijin ki kenan, amman saboda Allah ko d'an irin karar nan babu?"
"To shikenan wallahi bari in baku waje kafin ku tarar min kuyi min d'an banzan duka dan dai ni ba shuru zanyi ba, in naga abu dole inyi magana".
Ya mik'e ya fice daga palon yana fad'in kunga tafiya ta masoyan asali, koda yake duk burga ce tun da yau Soyayyar ta samo asali.
Ya fice yana dariya.

Yana fita Khadija ta sunkuyar da kai k'asa tana sauraran Aliyu dayayi shuru sai kace bashi ne yagama zuba yanzu ba.
Sunfi minti biyar shuru da alama Jinin sarautar ya motsa wa Aliyu Haydar.Can kamar daga sama, Khadija taji shi ya jifo mata tambaya, "Khadija kunyi hutu ko?"
"muryar ta a danyaye tace "yaya Aliyu ai na bar _America_ a nan B,U,K nake yanzu."
Cikin mamaki ya dube ta yace _"why?"_
Sam Khadija bata iya k'arya ba wannan dalilin yasa ta faiyya ce ma Aliyu biri har watsiya, ba ta boye masa komi ba dan gane da abinda ya faru tsakanin ta da Amatullah ba.
Murmushi Aliyu yayi kawai a hankali cikin izza yace mata "nagode da k'aunar ki a gare ni Khadija."
"hakika ke masoyiya ta ce ta asali tunda har kika zabe ni kika bar kawar ki, sai gashi kuma Allah ya dubi zuciyar ki yaba ki ni a matsayin miji, nikuma ya bani ke a matsayin matar aure, dan haka sai mu kara godewa Allah a bisa wannan zabi dayayi mana na alkairi."
Nan dai suka ci gaba da tattaunawa irin ta masoya, in da Aliyu ya d'aukar mata alkawarin kula da ita tsakanin sa da Allah har iya tsawon rayuwar sa. Khadija ta yi farin ciki sosai da jin hakan, inda a k'arshe ya shaida mata cewa zai aure sune ita da Amatullah saboda ita zabin mahaifiyar sace yayin da ita Khadija d'in ta zamo zabin mahaifin sa, yayi mata karyar hakan ne dan kada tasa wa ranta wani abu daban .
Ai kuwa ba k'aramin gigicewa Khadija tayi ba, kuka tasamai tana fadin taya ya zata yarda ta yi kishi da aminiyar ta, kuka sosai take yi tana fadin bazata iya ba, wannan ai abin kunya ne ana barin halas dan kunya.

Da k'yar Aliyu ya shawo kanta ta yarda, yakuma shaida mata cewa ita kanta Amatullah bata san shi zata aura ba dan haka ta kwantar da hankalin ta.
Haka suka ci gaba da hiran su daga k'arshe sukai sallama inda yacika ta da kudi, tayi mashi rakiya har zuwa motar su inda Yaron Malan keta mata tsiya Aliyu na rama mata da haka dai sukai bankwana cike da farin ciki Khadija nata yiwa Allah godiya daya cika mata burin ta na samun _Aliyu Rasheed Ganduje_ .

*************

Bayan k'wana biyu Aliyu da yaran Malan suka shirya suka nufi Abuja dan kai gaisuwa ga _Mr President_ cikin mutunci da karamawa aka amshe su, inda suka gaisa da _Mr President_ nan ma ruwa kawai Aliyu yasha, _first Lady_ Hajiya Asma'u ma tazo suka gaisa cikin mutunci, inda ta fice tana fadin bari ta turo masu Amatullah d'in.
Dama shi mahaifin nata tuni ya bar palon.

Aliyu ne ya mik'e yana fad'in "dan girman Allah Abokina kayi kamar yadda na umurce ka kada ka kofsa mun dan Allah Wlh kanada babban k'yauta idan har ka tafiyar da komi yanda ya kamata alkawarine wannan wallahi!".
"Dallah Malan ka fice kada tazo ta tadda ka nagaya maka zanyi aidai kasan ni ina girmama alkawari ko? So ka kwantar da hankalin ka bakada matsala."
Ficewa Aliyu yayi daga palon ya nufi mota ya zauna yana jiran fitowar Yaron Malan.

Amatullah wacce tasha k'walliya kamar zata gasar cin sarauniyar k'yau ta shigo d'akin bakin ta d'auke da sallama, nan Yaron Malan ya amsa mata tare da binta da kallo saboda ganin tsabagen kyau irin nata ga d'iri tuburkalla, da k'yar ya iya cewa "barka da shigowa gimbiya sarautar mata, dafatan nasame ki lafiya?"
Amsawa tayi bayan ta nimi kujera ta zauna, suka gaisa sosai yaron Malan ya dube ta yace masha Allah ashe dai Amaryar tawa k'yakkyawa ce, nayi wa Allah godiya, Amatullah ki godewa Allah kina da kyau sosai, cikin jin dadi Amatullah tace nagode!.
Daga haka kowa yaja bakin sa ya tsuke, saidaga baya Yaron Malan yashiga jefo mata yan tambayoyi tana basa amsa daga k'arshe yayi mata sallama tare da cika ta da kudi.
No rakiya batai masa ba tashige cikin gida zuciyar ta cike da murna tasami _handsome guy_ d'an gidan sarauta.

Koda uwar ta gaya mata su biyu zai Aura sam bata damu ba acewar ta mezai dame ta tunda tasan kowa da nasa makeken gidan aljannar duniya ita ai batada matsala kwata kwata Allah dai ya nuna mata ranar auran lafiya.
Uwar tace "wai ni Amatullah naga alamar kinma fimu matsuwa da wannan auran ne "
Dariya kawai tayi ta fice tabar uwar............

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: [4/5, 4:53 PM] FIDDAUSI SODANGI💅: [4/5, 2:45 PM] FIDDAUSI SODANGI💅: *KAINE SANADI* 6️⃣0️⃣to 6️⃣5️⃣

*WRITTEN BY :*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

*Godiya mai tarin yawa (ANTY SIS) wannan page d'in sadaukarwa ce a gare ki, hakika Sodangi tana alfahari dake a koda yaushe Allah yabar zumunci, nagode da gudun mawar ki agare ni*

Haka abin yaci gaba da kasancewa abu kamar wasa sai gashi k'aramar magana tazama babba, lokacin biki ya k'arato, shirye-shirye ta ko ina yinsa ake babu kama hannun yaro.
_Programs_ d'in da Amatullah tayi d'ai d'ai d'ai har guda shida kuma duka babu ango domin kuwa Aliyu ya sakar wa Yaron Malan komi shine angon Amatullah yayin da shi ya tsaya ma Khadija a duka _programs_ d'in da tayi. Yaron Malan yabawa Amatullah uzirin sa kan cewa abubuwa sunyi masa yawa shiyasa bazai sami zuwa can Abuja ba sai idan sundawo nan d'in

sun had'e, sam Amatullah bata damu ba sai hidimar da take tana wani rawar kan ita matar d'an sarki ana tayiwa k'awaye kankanba.

Ba k'aramin k'ud'i Yaron Malan ya sakar mata ba domin ta guda nar da hidin damun ta babu takura, ba k'aramin kuka kud'i sukayi ba a wajan sha'anin bikin ba, domin kuwa _first Lady_ zagewa tayi ta fidda y'ar tata kunya, kud'i kamar tsinto su suke.

Kayan da Amatullah kawai taringa sakawa ya isa mutum yagane anyi barnar kud'i a wajan, kaya ne masu tsadar gaske d'inkin su kawai ma ba a nan k'asar akayi ba gaba d'aya a waje akayi su.

Haka sukai ta gudanar da sha'a nin su har zuwa ranan alhamis inda _Mr President_ ya had'a kan iyalin sa sukayi gida watau kanon dabo tumbin giwa domin a gudanar da d'aurin aure a gida cikin dangi domin kuwa kowa yabar gida to gida ya barshi.

Rana bata k'arya saidai uwar d'iya taji kunya inji bahaushan mutum, a yaune aka d'aura auran *ALIYU RASHEED GANDUJE* da *KHADIJA MUHAMMAD DALA* sannan aka kuma d'aura na *AMATULLAHI AHMAD FAGE* da *ALIYU RASHEED GANDUJE* akan sadaki naira dubu d'ari acikin babban masallacin juma'ar da ke nan cikin garin kano, bayan sallar juma'a inda manya manyan sarakuna da yan siyasa da manyan y'an kasuwa suka cika ko ina, sai tarin abokan Aliyu gaiyya guda, kai wannan d'aurin aure ya sami halarta mutane masu yawon gaske, saidai muyi fatan ubangiji Allah yaba da zaman lafiya da zuri'a d'aiyaba.

bayan an k'are d'aurin auran ne gaba d'aya aka d'unguma zuwa gidan _Mr President_ domin gudanar da _reception_ na maza, domin kuwa mai girma gomna Muhammad Dala abokin sa ne na kud da kud, shiyasa suke gudanar da komi na bikin a tare.

"Amatullah wacce keta sharar kuka tun da safe babu irin rarrashin da _Anties_ d'in ta basuyi mata ba amman taki hakuri tayi shuru,uwar da kanta tazo tana ta aikin rarrashi amman ina tamkar ana dad'a zuga tane, nan tayi fushi ta k'yaleta.

yanzu ma kukan nata ne yakaru data tabbatar dacewar lallai zuwa yanzu ta tabbata matar Aliyu ta sunna wanda a iya tsawon rayuwar ta sau d'aya ta taba ganin shi kullum uzuri yake kawo mata baya zuwa.

haba saima kukan nata ya k'aru harda ihu, k'awayan ta dai sun saka mata ido suna kallon ikon Allah.

Su dai sun san ba auran dole za aiwa Amatullah ba na soyayya ne amman saiwani abu dakeyi haka su kam abin na Amatullah yafara basu haushi ya bar basu mamaki bata masu rai yake kawai, babban yarinya da ita tana abu kamar wata y'ar k'auye, ai ko yaran k'auye sun daina wannan yayin acewar su.

*************************

"Baba na mai kake nufi da wannan zance naka, duk yawan gida jan ka kace kai had'e matan ka zakayi a gida d'aya? D'ayan ma mafi k'aranci daga gidajan ka? Gaskiya Baba na wannan zancan banza ne, gidan nan yayi maku kad'an sosai, ai wannan gida ko mace d'aya bazan bari ta zauna ba bare har su biyu gaskiya!"

Cikin k'wantar da murya Aliyu yasoma magana, Allah ya k'ara maka nisan k'wana akwai dalilin daya sa zanyi hakan ne, amman bawai ina nufin a haka zasu ci gaba da zama ba a'a kawai zasu zauna ne na wani d'an lokaci sai in maida kowacce gidan ta daban.
Dan Allah mai martaba ayi min wannan laminin wallahi tsari ne mai kyau nakeso in tsara.
Dak'yar ya shawo kan mahaifin nasa ya amince masa da buk'atar tasa.
Cike da murna da farinciki mara adadi yabaro fadar.

**************

*DA DADDARE*

khadija aka farawa kaiwa gidan miji bayan ta sha fad'a da nasihohi masu ratsa jiki, kuka sosai take, tana jinjina yanda zatai zaman kishi da Amatullah aminiyar ta na kud da kud tun suna yara..
Surutu da tsegumi yasoma tashi a bangaran yan uwan Khadija da kawayan ta na ganin d'an k'aramin gidan da abokan ango suka kawo su matsayin gidan auran khadija kenan, mamaki da Al'ajabi kowa keyi, ganin surutun yayi yawa ne Amarya da kanta ta shaida masu cewa ai yace ba dadewa zatayi a nan gidan ba yana da dalilin kawo ta nan din zuwa wani lokaci, shiyasa kowa yaja bakin sa yayi shuru,
Abokan ango sunshaida masu ba a kwana gidan Amarya a tsarin masarautar su Aliyu, dan haka bayan wani d'an kankanin lokaci kowa ya watse aka bar amarya da halin ta.

**************

Amatullah ta fito sak Amarya abinta, sai k'yalli takeyi ta d'au k'walliya abin saidai Wanda yagani, idanuwan nedai suka kumbura alamar taci kuka ta gode Allah dama ga idanuwan nata tubarkallah.
Anty Amina kanwar _first Lady_ ce ta shigo d'akin ta kamo hannun ta suka fito d'akin domin ta kaita gun mahaifiyar ta da sauran dangi dan ai mata nasiha domin mahaifin ta _Mr President_ yace shida kansa zaikai y'ar tasa d'akin mijin ta.

Suna fitowa palo nan jama'a suka d'auki bud'a, wata abokiyar wasan Amatullah tace shakiyiyar banza kawai da iskanci ne yasaki lafewa kenan kinai mana kukan iskanci, dan kar ace kina zak'wad'i, dama kin gyagije abinki yarinya gidan Aliyu tamkar ankai ki angama, in kikayi tsiya kuma ince nafasa zaman d'akin, dariya sauran mutanan sukayi, janta Anty Amina tayi zuwa sama.

Hajiya Asma'u _(first Lady)_ da wasu k'awayan ta tare da y'an uwan ta su ka iske a zaune suna ta surutu akan gida d'aya da Aliyu yace zai hada matan sa, wai dan ma basu ga gidan ba

kenan, gaba d'ayan su suka bi Amarya da kallo nan d'akin ya dauki hayaniya kowa nafadin Masha Allah Amarya tasha k'yau,  kanta a k'asa ta zauna kusa da uwar ta a k'asa. Nan uwar tayi mata nasiha sosai tasa mata albarka, in banda kuka babu abinda Amatullah keyi.

Wata yar Hajiya Asma'u ce ta soma yima ta nasiha kamar haka:

"Da farko Y'ata nasihar da zan miki shine, kikula da shinfidar mijinki."

"Y'ata kikula da in da mijinki yafi so ajikinki".

"Y'ata kikula da abincin da mijinki yafiso."

"Y'ata karki bari mijinki yaji wari a jikinki."

"Y'ata gidin ga girmama mijinki."

"Y'ake yata karkikuskura kiraina yan uwan mijinki." "Yake y'ata kibi mijinki sauda k'afa domin aljannar ki na k'ark'ashin k'afar sa."

"Yake y'ata kifishi nuna farin ciki alokacin dayake farinciki, sannan idan yana bak'in ciki kifishi nuna bak'in cikin ki, ki k'wantar masa da hankali."

" Yake y'ata ki lura da lokacin cin abincinsa, idan lokacin yayi toki tanadar masa kafin ma ya iso, idan ya shigo kiyi masa tara irin ta darajawa ki gabatar masa da abincin sa basai yace ina abinci naba?"

" Ya ke y'ata ki lura da lokacin da mijinki ke jin bacci ki barshi ya k'wanta ya huta kada kidamesa." "Yake y'ata ina horan ki dayin ado, ki lura da inda yafi kallo ajikin ki da zarar yashigo cikin gida."

" yake y'ata ki kiyaye kunnin mijin ki, kada kibari yaji mummunar zance daga bakin ki."

"Yake y'ata maganata ta k'arshe da zan gaya maki shine ki guji bakin kishi! "

Allah yabaku zaman lafiya da zuri,a dayyiba Ameen.

Wata k'awar Hajiya Asma'u mai suna Hajiya Fatima tace "Amatullah kina jina ko?"

"  ki rike wayan nan abubuwan dazan gaya maki insha Allahu zakiyi alfahari da auranki,  zaki sami mijin ki a tafin hannunki batare da boka ko mallan ba dan Allah Amatullah kirike wayannan abubuwan banda k'iuya, _please!_"

"Nan da sati biyu nake so ki fara wannan abin da zan gaya maki.
Kina jina ko? "

"ki sami tumatir da kankana,  ki markad'a shi a blanda,  sai ki samu dabino mai k'yau kicire masa y'ay'a kisaka a tukunya da ruwa kadan ki dafa shi ya dahu sosai luguf,  saiki Dame shi ki zuwa a markadaddan tumatir da kankanar nan kisami madarar ruwa da zuma ko suga kisa aciki ki juya sosai ki shanye abinki kinji ko ki jure yin hakan dan Allah,"

"Sannan kuma ki juri yin kunun dabino,  kisami dabinonki mai k'yau ki cire k'wallon sai ki jika shi harsai yayi taushi sosai,  saiki markada a blanda ki zuba madarar ruwanki da zuma ki ringa shan abinki,"

"Sannan kuma ki yawaita cin k'wad'on zogale da dafaffaen k'wai da tumatir,"

"Ki yawaita cin dabino wanda bai busheba da ruwa,shima yana taimakawa sosai kinji ko

Amatullah?"

"Sannan kuma ki sami madarar ruwanki da k'wai ki kada shi sosai harsai yabar kumfa ki shanye abin ki tas,"

"Saikuma Abu na k'arshe idan Kin kusa gama period dinki kisamu alkama, a niko maki ita sai ki soyata sama -sama, har yayi ja, dakinga kin kusa gama period dinki sai ki dama shi kamar salala ki sha shi da nono sau uku, shima yana taimakawa kinsan period yana tafiya da abubuwa dayawa."

"Amatullah Dan Allah kada kibani kunya ki juri yin wayan nan abubuwan dana lissafo maki su, idan kikayi wannan bayan kwana biyu kuma saikiyi wannan insha Allah zanzo gidan naki da yardar Allah, kuka sosai Amatullah keyi ga kunya tamkar ta nutse k'asa.

Haka dai sukai ta yi mata nasiha har zuwa lokacin da mahaifin ta ya tashi tafiya da ita. _Mr President_ da kansa ya sakata a mota ya nufi gidan Aliyu da ita wanda yake a GRA tsayawa fadin tsarin gidan bata lokaci ne gidan yahadu karshe, saidai d'an karami ne. hannunta mahaifin ya ruk'o har zuwa palon.
Aliyu ya taso da sauri ya taresu, amman sam Amatullah bata lura shine ba domin kanta a kasa yake, nan khadija ta gaida _Mr President_ cikin girmamawa, amman duk da haka Amatullah bata dau murya ba domin ita hankalin ta ba a kwance yake ba.
ya amsa cikin sakin fuska sannan ya fa dayi masu fad'a mai tsuma zuciya Amatullah kuwa kuka kawai takeyi tana karawa,
“Haka yaringa gaya masu yanda zaman aure yake a musulunci. da abinda ya halatta miji yayima matar sa da wanda ya halatta Mata tayiwa mijinta. Yacigaba dacewa Aliyu ga amanar Amatullah nan nabaka. Don Allah ka kular min da ita ka kula da hakkinta daya rataya a wuyanka kada kaci amanar ta kada ka zulunceta idan taimaka kuskure ka ganar da ita cikin ruwan sanyi yadda zata fahimta idan taimaka laifi Wanda yafi karfin hukuncin ka Dan Allah kanimeni koda a waya ne. Nikuma in allah ya yarda zanyi maka maganin abin koma menene. Yajuyo kanta yace kekuma Amatullah hakika nayi murna da farinciki da samun ya mai biyayya kamar ki Ina alfahari dake nagode Allah yasaka maki da alheri Dan girman Allah Amatullah ki zauna kiyi zaman aure Dan bakida abinda zakimin Wanda yawuce kiyi zaman aure Amatullah kiyi biyayya ga mijinki yinayi Bari na Bari shine zaman aure kada ki sake mijinki yakawo min karar ki kosau daya ne kinji nagaya maki kada insake inganki dasunan yaji! Kizamo mai boye sirrin mijinki danaki. Kada ki tozarta mijinki koda sau daya kidaure duk abinda zai shiga tsakanin ku kumagance ma kanku shi. Sai dai in abin yafi karfinku sai Ku gayama nagaba daku. Amatullah kada kisake mijinki yakawo min kararki inakara shaida maki idan na bincika naji kece bakida gaskiya to wlh Zan mummunar Saba maki.
kinsan halina sarai.
aure ba abin wasa bane kiyi biyayya aljannarki na karkashin kafarsa saiya daga zaki shige kina jina ko?"
"Cikin kuka tace eh!"

“Yace ke kuma khadija kema ga amanar Amatullah nan nabaki dama ku aminai ne kun riga

kunsan halin junan ku,
dole sai kunayi kuna hakuri da junan ku, saboda zomu zauna zo mu saba ne.

Dan girman Allah Ku zauna Ify kuyi kishi irin na matan sahabbai ba irin kishin haukan da akeyi yanxu a wannan zamanin ba Ina fata nasihata ta shige ku kuma zakuyi aiki da ita! Gaba daya suka amsa da insha Allah sam Amatullah bata gane muryar suba har a wannan lokacin dan hankalin ta a tashe yake duk idon ta duk sun kunbura da kuka.

Amatullah kuka kawai take tamkar Zata shide. Ahaka yayi masu sallama yatafi,

” Aliyu ya raka sa har mota, yana fita Khadija ta mike tsaye ta shige d'akin ta dan ta lura sam Amatullah bata shaida suba.

mik’ewa Amatullah ma tayi itama tanufi nata d’akin dan ganin d'aki biyu ne kawai a cikin gidan, dan haka tasan tabbas nata ne d'ayan,

Wani bangare na zuciyar ta na mamakin yaza ai ya aje su nan gida saikace akurki.

Aliyu nadawowa ya nufi d'akin Khadija ya shaida mata yana son ganin su a Palo daga haka ya fice abin sa yanufi palon ya zauna, wayar _land-line_ na palon ya d'auka ya kira Amatullah wacce tuni tabar kukan tama tube tana shirin shiga wanka ne taji wayar na kara, kamar karta dauka sai sai ta tabe baki ta dauka kawai.

murya kasa kasa ya ce "kifito palo muna jiran ki ya aje wayar wani iri taji muryar tasa ba yanda tasaba ji ba sai dai ta share kawai ta shige kewaye tayi wankan ta, saida ta bata lokaci sosai sannan tafito ta tsaya gaban madubi ta karaci k'alailaitar ta tukun, sannan tasa kaya ta buga dauri ta lullube kanta da babban mayafi ta feshe Jiki da turare.

Cikin tafiyar ta ta tak'ama da isa ta iso palon, tafiya take a hankali gaba d'aya jikin ta babu inda baya juyawa, kanta a k'asa tana k'ara gyara lullubin kanta, kujera ta nima ta kame abin ta tare da d'aura k'afa d'aya bisa d'aya tana kallon farcan ta daya sha jan farce alamar tana fashin sallah.

Aliyu wanda ke zaune kujera daya shida Khadija ne yayi gyaran murya cikin kakkausar murya yace "ke ba a koya maki gaida mutane bane a gidan naku?"

"naga alamar baki da tarbiyya ko?"

Khadija ce ta d'an zungure sa alamar ya bari, yayin da Amatullah tayi wani irin zabura ta mik'e tsaye tana zare ido yayin da mayafin kanta yayi k'asa. Shima tsaye ya mik'e dan ya shirya ma hakan dama, a hak'e yake dama da shanya su data yi niyyar sa yayi k'asa-k'asa da ita idan ta kawo masa raini.

Cike da k'arfin hali tafara fad'in "uban wa ya kawo ka gida na! Taya ma akai har masu gadi suka barka ka shigo?"

"lallai yau zaka raina kanka wallahi wallahi tunda har ka kawo kanka da kanka cikin gidan nan ai dama nayi alkawarin sai na nimo ka duk inda kake a fad'in kano domin in koya maka darasin rayuwa in nuna maka cewa Amatullah ba tsarar ka bace tafi k'arfin matsiyaci irin ka"....... Hannu ya d'aga da niyyar ya sharara mata mari da sauri Khadija ta rik'e hannun nasa tana fad'in "haba miji na! Taya za ai ka biyewa mace macan ma matar ka ta sunna wacce kake da k'arfin iko a kanta har ta haddasa maka damuwa a cikin wannan dare mai cike da tarihi? Karfa ka manta wannan daran alkairi ne a gare mu, dare ne wanda zamu nunawa Allah farin cikin mu muyi

masa godiya mu gode masa daya nuna mana wannan rana da ranmu da lafiyar mu, saboda haka kacire kowacce damuwa a ranka gwarzon miji na, haba Aliyu gadan ga k'usar yak'i,  haba Yarima d'an sarki Angon Khadija Muhammad Dala da Amatullah Ahmad Fage, haba miji na da babu tamkar sa a duk cikin mazajan duniya, haba Aliyu Haydar d'an sarki kuma sarki mai jiran gado insha Allahu.
  A hankali ta saki hannun sa tana kallon cikin idon sa yayin da take sakar masa murmushi mai sanyaya zuciyar masoyi, a take ya jawo ta ya rungume zuciyar sa nayi masa wani irin sanyin dad'i...............

DEDICATED TO
 KUBRA USMAN BALA
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI*  6️⃣5️⃣to7️⃣0️⃣

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

Zuwa yanzu Amatullah tagama fahimtar meke faruwa, watau Aliyu ya aure tane dan ya nuna mata iya karta shine ya had'a ta da khadija saboda yana so ya kunsa mata bak'in ciki, lallai kuwa yau zaiga d'anyan kai a cikin akurkin gidan nan nasa.

Tamkar wata mahaukaciya Amatullah tayi kansu tana fad'in "wallahi wallahi baka isa ba Aliyu kayi kadan daka aure ni! ka dube nifa, nayi maka kama da matar matsiyaci irin ka?"
"Wallahi kodai ka sake ni kokuwa inzamo ajalin ka dan wallahi wallahi sai nayi maka abinda baka taba tunani ba matsiyaci kawai da'n iska! Nizaka rainawa wayau wallahi bazan yarda ba dole in dau mataki a kanka. "

Da gudu tayi hanyar d'akin ta ta rufe tana rusar kuka.

Aliyu ya saki Khadija rannan nasa a bace yace "khadija daga yau sai yau bana so ki k'ara hana ni yin abin da naga dama akan yarinyar can, in dai har kina son farincikina dole ki bani had'in kai dan mu koya mata hankali, in kika lura sam yarinyar bata da tarbiyya dan haka kibani had'in kai mu sai tata tadawo hanya kin gane ko?"
"shikenan miji na na fahimce ka Allah ya bani ikon yima biyayya."

"kije ki shirya lokacin zuwa _dinner_ d'in yayi, kayan dana baki d'azu su zakiyi amfani dasu, jeki d'auko min na wancan yarinyar su ne a d'aya jakar."

D'akin Amatullah ya nufa bayan khadija takawo masa jakar, bubbugawa ya shiga yi da k'arfi amman taki budewa da alama ma ta zare _key_ d'in a jikin k'ofar, d'akin khadija ya koma ya nimo gudan _key_ d'in ya bude d'akin ya shiga.

Tana k'wance tana kuka tamkar zata shid'e,
Cikin kakkausar murya yace "kee! Ki tashi ki shirya karki batawa mutane lokaci dallah!.

D'if tayi tamkar ba itace ke rusa kukan ba dan a ganin ta ai rainin wayau ne ma yaga tana kuka.

K'ara daka mata tsawa yayi yace "badake nake magana bane! Nace ki tashi ga kaya nan ki saka zamuje _dinner_ da abokai na suka shirya mana, ya kare maganar tare da wulla mata jakar a fuska."

Wani irin mugun kallo tayi masa da idanuwan ta dasukai jawur cikin tsiwa tace "uban waye zaije k'azamin _dinner_ ku ta k'ananan yara y'ay'an talakawa matsiyata masu warin baki?"
"to idan ma mafarki kakeyi ka farka ni ba tsarar ka bace kasani, dan haka ka kiyaye ni magana in bata takarda ta bace to bana buk'atar kayi min ita kaji nagaya maka!".

Murmushin mugun ta yayi ya haye gadon kamar kiftawar ido ya murde mata baki da hannun sa yana kallon cikin idon ta yace" k'ara maimaita kalaman ki inji?"

Azaba yasa takasa magana a gigice ta kamo hannunsa ta gartsa masa wani mugun cizo, da sauri yasake ta tare da kifa mata wani wawan mari, "ni kika ciza?" lallai zanyi maganin ki yau d'in nan, kafin tayi wani yunk'uri tuni ya had'e bakin su waje d'aya ya lalubo harshan ta ya gantsara mata wani uban cizo a harshan da iya k'arfin sa, ai gaba d'aya Amatullah ta shid'e dan tsananin azaba tafi minti biyar a haka kafin ta dawo haiyyacin ta, ta rik'e bakin ta hawaye nabin k'uncin ta tana kallon sa tana tunanin abinda zatai masa, lallai yau ta k'ara tabbatar wa Aliyu mugu ne baida imani, bata k'ara tabbatar da hakan ba sai da ta shafo harshan ta taga jini, baki ta bud'e zatai magana amman ta kasa dan azabar zugin da bakin ta keyi.

Murmushi yayi yace "gobe ma ki k'ara kinji?"
"Kuma kitashi ki shirya kafin inyi k'asa k'asa dake anan!."
A hankali ta tashi tasoma k'wabe kayan jikin ta a gaban sa ko kunya bata jiba daga ita sai pant da bra da sauri ya kauda kansa tare da ficewa a d'akin har yana tuntube, tsaki taja tace "d'an iskan banza ai da ka tsaya!"
Kawai zata bisu wajan _dinner_ d'in ne dan ta nuna masu iyakar su acewar ta kenan a zuciyar ta.

Jakar da ya wurgo mata ta bud'e da niyyar idan kayan ciki basuyi mata ba wallahi bazata saka ba, sai dai tasa nata kayan, tana bud'ewa taga wata
doguwar riga na _Lace_ mai d'ankaren tsada, wanda _Style Temple_ ta d'inka, sai set d'in zinari shima mai kyau, takalma ne na alfarma masu tsada da _clutch_ bag dinsu a hade.
Sai wani d'an goggoro mai azabar kyau, sai kuma mayafi mara nauyi mai kyau shima kalar _lace_ d'in kayan dai sun had'u ba karya, ita kanta tasan kayan sunyi kyau gasu kuma kalar da ta fi so ne, shiyasa ta ciro su ta soma sawa tana wani yatsine fuska.

Wohoho.... Wani kaya sai amale! Wai kuwa kunga yanda Amatullah tayi wani irin bala'in k'yau cikin kayan? Abin sai wanda yagani, kayan sun zauna d'as a jikin ta tamkar a tare aka halicce su, k'ugun nan yafito tamkar zai fasa rigar kai masha Allah Amatullah kam akwai _shape_ mai k'yau tubarkalla.
Zama tayi ta tsara k'walliya nagani na fad'a tamkar wata sarauniyyar k'yau.
Gaskiya ko d'an bakin ciki bazai ce batayi k'yau ba kam.
Goggoran ta saka a kanta bayan ta gama kwalliyar tasa d'an hannun da yan kunni tare da abun wuyar harda wani sarkar k'afa, nan da nan tak'ara haskawa, kin saka mayafin tayi tayi wurgi da shi bisa gadon.
D'an pos d'in dake had'e da kayan ta d'auko wanda ke shake da kudi a ciki, sai wayar ta data d'auko tafito palon tagan su a tsaye alamar ita suke jira, itama khadija irin shigar Amatullah ne a jikin ta sai dai kalar ya banban ta.
Aliyu ma Yayi bala'in yin k'yau abin dai ba a cewa komi.
Aliyu bai san sanda ya had'e miyau ba ya d'aure fuska had'e da buga mata tsawa "kije ki saka mayafin ki baza ki bini a haka ba, bakida hankali ne?"
Tsaki tayi ta koma ta d'auko mayafin ta yafa a kafad'ar ta Aliyu yaji kamar ma yace bazata ba dan shidai bai ga amfanin wannan d'an iskan mayafin ba.
A fusace yace "wai ke bakida wani mayafin dazaki iya amfani dashi ne dole sai wannan gantalallan ko baki san ke katuwa bace mara tsarin gani?"
"kidube khadija mana ya fad'i yana nuna mata khadijan da hannun sa, baki ga yanda nata yai mata dai dai ba zar sha'awa?"
"Amman ke abu wani gandandan dake babu ko k'yawun gani!"
Rai a bace Amatullah tace "ai kaine gantalallan daka d'in ko shi! Zaka gaya wa mutane maganar banza! Ai wallahi wallahi k'arya kake kace bani da tsari dan kasan"...........Yaron malan ne yashigo yana fad'in "Aliyu kuna fa batawa mutane lokaci kufa ake jira tuntuni dare nata yi saboda Allah".
Wani mugun kallo Amatullah tayi masa tace "watau kai ne munafukin da aka hada baki

dakai a ka cece ni ko?"
"to wallahi Allah bazai barku ba d'iyan matsiya ta kawai! "
Ido Yaron Malan ya zaro yana jinjina rashin mutunci irin na Amatullah, alama Aliyu yayi masa dayayi shuru karyace komi, dan haka Yaron Malan yafice ransa a bace.
*Ficewa Aliyu yayi hannunsa cikin na khadija, Amatullah ma ta rufa masu baya.
Yaron Malan ne ke tukin yayin da Aliyu da matan shi ke baya sun saka shi a tsakiya, tsawon minti biyar suna tafiya Aliyu da khadija suna ta hira k'asa-k'asa ko Amatullah da ke kusa dasu bataji, yawani k'wanto jikin khadija kamar zai shigar da ita cikin sa, zuwa can khadija tasoma wani k'yalk'yala dariya Aliyu nayi mata cakulkuli tana wani gantsarewa ko kunyar Yaron Malan basa ji can ya fad'a jikin ta yana ci gaba dayi mata wasa tana k'wasar dariya ya manne ta a jikin sa yana sakar mata _kiss_ ta ko ina, dariyar kamar zata shid'e, Amatullah taja wani wawan tsaki tace "iskancin banza kawai tambad'ad'd'u kawai! Wayanda basu san ciwon kansu ba!"
Aliyu daga shi har khadija tamkar ma basu san Allah yayi Amatullah a wajan ba, Aliyu ya ci gaba da wasa da matar sa haryana fad'in Amatullah ta d'an k'ara matsawa ta basu waje ta matse su.
Sam Amatullah ta kasa kauda idon ta a kansu bak'in ciki, takaici tamkar ta had'e zuciya ita kan ta bata san meye abin jin haushi ba dan suna wannan iskancin ba.
Yaron Malan kuwa tamkar ma babu shi a matar duk da yana sane da abinda ke wanzuwa yana jinjina iskanci irin na Aliyu, lallai yanaso yasawa yarinyar nan hawan jini.

A haka suka isa wajan aka soma gudanar da komi cikin tsari inda Amatullah tazama yar kallo tama kasa aiwatar da abin da tayi niyya ahaka har taron ya watse inda Yaron Malan ya maido su gida.
Ko sauraran su batayi ba ta shige d'akin ta ta rufe tare da barin mukullin a jiki, wayar ta ta d'auka ta kira uwar ta fashe da kuka tamkar ranta zai fita, a rikice uwar ke tambayar ta abin da ke faruwa, takasa magana illa kukan da ta ke ci gaba dayi.
Da kyar ta soma magana "wallahi _mum_ bazan iya zama gidan nan ba wallahi bana son shi na tsane sa _mum_ ki taimake ni ya sake ni wallahi bazan zauna ba"...... Wani irin tsawa uwar ta daka mata, "wani irin maganar banza ki keyi haka Amatullah?"
"to wallahi ni babu ruwana badani ba a wannan rigimar dakike nima ki d'aukowa kanki ba, gara ki rufawa kanki asiri ki kwantar da hankalin ki kiyi zaman aure kamar kowace mace, amman ni babu ruwa na Karma kisake mahaifin ki yaji wannan mummunar zance a bakin ki, kinji nagaya maki!"
Daga haka ta katse wayar ta, Amatullah ta mik'e ta zare _key_ d'in ajikin k'ofar ta nimi waje ta boye shi sannan ta dawo ta zauna ,
tasaki kuka mai cin rai tana niman mafita, haka ta kwana a zaune tana wannan kukan mai cin rai.
Cikin rashin k'warin jiki ta mik'e ta nufi _toilet_ ta d'auro alwala tun kafin ta fito taji wani masallaci suna k'ok'arin tada ik'ama.
Da sauri ta shimfid'a abin sallah tare da saka hijjabi ta bisu, domin tana jin karatun su rad'au tamkar a cikin d'akin ake yi.
A in da tayi sallar anan bacci mai nauyi ya d'auke ta, sama-sama cikin bacci taji ana bugun k'afar ta da k'arfi tare da fad'in "ke! Ke! Baccin uban me kike har zuwa wannan lokacin?"

A hankali ta bud'e idon ta tana ganin Aliyu ne da sauri ta mik'e tamkar wacce aka jonawa wutar lantar ki, ta d'aure fuska tamau, ta kalle shi sama da k'asa taja tsaki, tare da fad'in "uban wa yace maka ana tashi na daga bacci?"
"kokuwa salon ka jaza min ciwon kai ne?  Har kake taba min k'afa! To wallahi Allah ya isa na daka taba min k'afa da kazamin hannun ka!"
Murmushin mugunta Aliyu yayi yace "karki damu y'an mata har abinda yafi k'afa nakusa fara tabawa kici gaba dayi min iskanci daidai nake dake fitsararra mara kunya, da alama ma kafira ce ke hala baki sallah?  Dan banga alamar kinyi sallah ba yau d'innan."

"kaji gantalalle! Ni da kai waye za a kalla acewa kafiri?"
"Wallahi ka rubuta min takarda ta in tafi gidan mu kaji nagaya maka!"

Dariyar mugunta Aliyu yayi harda tafa hannu, ya zo ya fad'a bisa gadon ya na k'yalk'yala dariya, daga ni kasan na mugun ta ne zalla.
Can ya d'an tsagai ta da dariyar yayi ruf da ciki a kan gadon, ya d'ago kai yana kallon ta yace.
"yaro yaro ne, bai san wuta ba sai ya taka.
Bari na fad'a maki, idan kina tunanin zan rabu da ke to gara ki cire wannan a zuciyar ki, ki watsar, dan yanda kika shigo gidan nan to babu mai fidda ki sai sai dai mutuwa."
"Shawarar da zan baki shine ki shirya zama da matsiyaci kamar yanda kike fad'a."
"Wallahi Aliyu baka isa ba kayi kad'an, wallahi na tsane ka kamar yadda na tsani mutuwa ta.
Kuma yazama dole ka sake ni tunda ba uban ka bane ya"....    Bata k'arasa fad'a ba ya sauke mata wani gigitaccan mari ji kake tasss!!!

Da sauri ta dafe kuncin ta, tsabar taurin kai irin na Amatullah sai cewa tayi "uwar kace ka mara d'an iskan....." wani marin yak'ara saukewa d'ayan kuncin nata a haukace taci kwalar sa tana sake d'ura masa ashar.
Hankad'a ta yayi fan yaga idan yabiye mata sai yayi mata illa.
Cikin kakkausar murya yace  _(This is my last warning to you)_ wallahi wallahi duk rannan dakika kuma zagi na sai na baki mamaki wallahi.....
Katse shi tayi da fad'in sai dai mubawa juna mamaki wallahi Aliyu!  Kayi kadan kabani mamaki mu zuba nida kai cikin gidan nan tabbas za a k'washi gawar mutum d'aya koni ko kai shege ka fasa...............

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA
[4/11, 6:47 AM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI* 7️⃣0️⃣to7️⃣5️⃣

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

_Masha Allah My Mentor! Hakika ina alfahari dake a koda yaushi, dole ne Sodangi takawo jinjinar ban girma a gare ki_ *KHADIJA SIDI* _hakika kin cancanci yabo, nagode da sadaukar war dakika min na littafin ki kacokan mai suna_ *BINTU DIYAR BAYI* _nagode sosai Allah yabar so da kauna Sodangi tana matukar kaunar ki fiye da tunanin ki._

Bai k'aracewa da ita komi ba cikin tsananin bacin rai yafice a d'akin, yana fita ta zube a k'asa ta soma raira kuka, wani irin tsanar Aliyu take ji har a zyciyar ta, tabbas yau ta k'ara tabbatar wa cewa tashigo cikin sabon rayuwa.

Sai da ta gama raira kukan ta mai isar ta sannan ta d'auko wayar ta tashiga kiran layin uwar sai dai abin takaici a kashe layin yake, nan ranta yak'ara baci, a take ta tuno da Anty Ameena har ta soma kiran layin sai tayi sauri ta kashe dan zuciyar ta bai bata ba ta tuno da nasihar ta a

gare ta inda take fad'in.

Amatullah na, ki kasance mai hakuri da juriya, sannan mai boye wa mijin ta sirrin sa.
Ba komi ne zai faru kice zaki buga ki sanar da wani halin da kike ciki ba, ki daure ki cije, shi zaman aure ya gaji hakan, dama akan hakuri ake yin sa, daga kai har mijin naka, shi yayi hakuri dake kema kiyi hakuri da shi.Allah ya tsinewa mace mai tona asirin mijin ta, musamman wajan sirrin ma'aurata.
Don haka Amatullah na kizama jaruma mai juriya akan duk wani k'aluballe dazaki fuskan ta a gidan zaman auran ki, dole ne zaki ringa ganin abubuwan takaici wayan da zasu tsallake tunanin ki, amman idan kikayi hakuri wata rana sai labari.
 Duk wata mace da kika ganta gidan mijinta, to sai ta had'a da hakuri, don haka koni Amatullah ban yarda kigaya min duk wani abu dake gudana a gidan auran ki ba, matukar kina so muyi shiri nida ke.
 Kuka ta sake fashewa da shi harda ihu kamar wata tababbiya.
 Dole kiyi masa biyayya ga dukkan abinda ya umurceki kiyi matukar bai sabawa shari'a ba, domin a k'ark'ashin sa kike, don sai ya d'aga k'afar sa sannan zaki sami aljannar ki, tunda auran nan dai yariga ya kullu dole kiyi hakuri da juriya babu yardda zakiyi, don kisamu ki dace miji ba abin wasa bane.
 A Karo na biyu tasake tunawa da nasihar mahaifiyar ta.
 Ajiyar zuciya mai k'arfi ta sauke ta tashi ta shiga _toilet_ ta shek'a wanka tafito tayi ado mai d'aukar hankali sannan ta bud'e k'ofa ta fice palo.
 Wani d'an k'aramin _fridge_ ta ci karo da shi kai tsaye ta nufe shi ta bud'e, ido biyu tayi da mutumin ta watau _fresh milk_ nan ta d'auko shi ta d'auki kofi ta tsiyaya ta soma sha tana lumshe ido, alamar yana mata dad'i wani irin sanyi ne ke ratsa mata mak'oshi.
 K'amshin turaran Aliyu ne yacika mata hanci da sauri ta dube shi daga shi sai guntun wando sai y'ar shimi ta maza da sauri ta d'auke idon ta bayan ta watsa masa mugun harara.
 Da sauri ya k'arasa inda take ya amshe kofin yana fad'in "uban wa yabaki izinin sha min madara?"
 "uhmm?"
"to ki sani bashi kika sha saikin biya ni!"
 Tsaki taja masa tabar wajan ta nimi kujera ta hard'e tana karkad'a k'afa.
 Dagani kasan kiris take jira.
 Wayar Aliyu ne yashiga ruri dama a hannunsa yake da sauri ya d'auka ganin Fulani ce ke kiran.
 _"Hello"._
_"ok_ babu laifi su shigo kawai "
 Ya dubi Amatullah yace "Allah ya soki yau fulani ta hutassheki ta aiko da abinci da yanzu sai kin shiga _kitchen_ kinyi mana _breakfast_ dan Khadija ba ta da lafiya bazata iya girki ba."
 Wani mugun kallo ta watsa mashi bata ce komi ba.
Suna cikin haka Sarkin gida ya shigo tare da wasu barori su kusan shida kowanne d'auke da hadaddiyar kula mai kyau,
 Bisa _dinning table_ suka shirya su reras, gwanin ban sha'awa, nan suka zube suka soma kawo gaisuwar su gun Aliyu da Amatullah.

Bayan sun amsa sarkin gida yayi waje yayi masu sallama, yayinda barorin suka nimi waje suka kame tamkar wasu gumaka.
Aliyu ne ya nufi _dinning table_ d'in ya zauna, nan Amatullah ma ta taso dan yunwa take ji, da sauri biyu daga cikin barorin suka iso gun jikin su na rawa suka shiga bud'e kulolin, nan wani hadaddan kamshi bai bala'in dad'i ya daki hancin Amatullah bata san lokacin da ta had'e miyau ba.
Nan suka dubi Aliyu suna fad'in "Allah ya k'arawa Yarima lafiya meza a zuba maka?"
"duk abin da zata ci nima shi zanci!"
Abinci ne na alfarma babu wanda babu aciki, tun daga kan na gargajiya harna turawa da larabawa duka gashi nan birjik.
Duk'awa d'ayan tayi tana fad'in "Allah ya taimaki Amaryar Yarima d'an sarki Allah ya k'ara maki lafiya Amarya ke nake sauraro ki bani umarnin me kike so kici?".
Yatsina fuska Amatullah tayi ta gyara zama cikin isa da mulki ta shiga zaiyyano mata abinda zata ci cikin tak'ama da izza.
Cikin jin dad'i tace "Allah ya taimake ki uwar d'aki na anyi an gama da wannan dama dana samu."
Nan ta shiga zuzzuba masu ta turawa kowa a gaban sa, sannan ta duk'a tace.
"A kammala lafiya"
Nan suka bar palon gaba d'ayan su,
Nan Aliyu yayi mata wani irin kallo yace "ina fata kinsan cewa ni angone domin kuwa jiya nayi kwanan farinciki, don haka yazama dole ki taso ki ciyar dani in koshi kafin kicika naki cikin ina fatan kin fahimceni?"
Wani mugun kallo tayi masa tare da murgud'a masa baki tace "ni ba a koya min haka a gidan muba dan haka kada Allah yasa kaci yunwar cikin ka ya kashe ka!".
Taja _plate_ d'in ta gaban ta tashiga cin abincin ta cikin kwanciyar hankali.
Da k'arfi ya damki hannun nata harsai datayi k'ara yace "ai nan ba gidan ku bane, gida nane nike iko dake dan haka dole kimin abunda nakeso".
"baka isa ba kayi kad'an!"
"ta fad'i kanta tsaye."
Hannun ta yasaki dan hango khadija dayayi tana tahowa, a hankali take tafiya tana dafe bango kamar wata mai koyan tafiya sai wani cije baki take yi kamar zatayi kuka.
Da sauri Aliyu ya mik'e ya tare ta ya rik'o ta a jikin sa suka k'araso yaja kujera ya d'ora ta kamar wata y'ar yarinya yanai mata sannu.
Wani dogon tsaki Amatullah taja tamkar harshan ta zai katse ta dalla masu harara sannan ta d'auke kai taci gaba da cin abincin ta.
Matsowa yayi da tasa kujerar ya had'e su waje d'aya yaringa dibo abincin sa yana bata a baki shima yana ci, can ya dube ta ya wani rungume ta a jikin sa yana fad'in
"nagode nagode khadija."
"hak'ik'a jiya kin shayar dani farinciki, kin d'ad'ana min daddadan zuma a baki, bani da abinda zan saka maki dashi illa inringa yi maki addu'a Allah ya shayar dake ruwan alkausara, ina yi maki fatan alkairi a rayuwar ki khadija Allah yasa ki gama da duniya lafiya. "
"Ameen mijina, ina alfahari dakai hakika kai gwarzon namiji ne da babu irin ka a duniya."
"Allah yabar mu tare yaraba mu da sharrin makiyi da mahassada."

"Ameen ya rabbi matata."
"wajan ya daina zafi kuwa?"
Yafadi yana kallon cikin idon ta yana kuma satar kallon Amatullah wacce tayi kicin kicin da fuska tamkar zata fashe.
  Kunya ne yakama Khadija ta mik'e tana wannan tafiyar tata mai kama da tatata.
  Da sauri ya sunkuce ta kamar wata y'ar bebin roba yana fadin muje inmaki tausa ai dole akwai gajiya dan kin nuna jarumta sosai waiii mace haka kamar zuma waiii wannan ai shine cakwala dadin.
   Ya shige d'akin ta da ita ya bugo k'ofar da k'arfi da k'afar sa.

Tsaki Amatullah tayi ta tashi tabar abincin nan ta shige d'akin ta zuciyar ta tamkar zata fito waje.
    Wajan awa d'aya da rabi taji ana ta buga mata k'ofa a sakwanne ta bud'e, ido hudu sukai da Aliyu sanye cikin manyan kaya farare tas da su, babbar riga da yar ciki sai wando, kansa sanye da hula sai kamshi yake da ka ganshi kaga sabon ango,
   Duk da bai burge taba amman tasan yayi kyau matuka.
   "zanje fada mu gaisa da mai martaba nida Yaron Malan,"
"Ko kina da saka'o?"
  Harare ta galla masa ta shige ta barshi nan rike da k'ofa a hannu.
  "bazan samu koda d'an _kiss_ bane wanda zaisa intafi cikin nishadi ba?"
 Ya fad'i cike da zolaya.
  Wani irin shan kunu tayi ganin rainin wayan nasa Yayi yawa.
  _come on_ ke nake jira.
A fusace tace "dallah Malan kabar min k'ofa insha iska angaya maka ni y'ar iska ce irin ka banza d'an tasha!"
  _ok_ to bari in shigo in nuna maki halin iskancin nawa!
  Ko kad'an batai tsammani ba sai ganin shi tayi ya shigo cikin d'akin da k'arfi ya fisgo ta jikin sa ya had'e bakin su gu d'aya yashiga shan shi irin na mugun tar nan hannunsa na kokarin zuge zip d'in rigar ta........

*DEDICATED TO*
*KUBRA USMAN BALA*
[4/11, 3:52 PM] +234 703 962 5239: *KAINE SANADI* 75to80

*WRITTEN BY*

*FIDDAUSI SODANGI*

*STORY BY*
*KHALISAT HAYDAR*

*®NAGARTA WRITER'S ASSOCIATION (NWA)*

_Wannan shafin naki ne_  *Eeesha Bagwai* _nagode da soyayyar dakike nunawa wannan littafi nawa, dan haka na sadauk'ar da wannan shafi a gare ki, ina godiya matuk'a Allah ya bar k'auna._

Da k'arfi taci nasarar ture sa ta tattaro miyan bakin ta ta watsa mashi a fuska, sannan tasoma sababi, "wai kai Aliyu wani irin d'an iskan mai rai ne?" "Meyasa baka da buri a kullum sai nason ka taba min jiki?"
"  To wallahi bari kaji ingaya maka wannan tsadaddan jikin nawa yafi k'arfin ajin ka wallahi

wallahi!  Dan haka koda wasa kada ka k'ara gigin taba min jiki da kazaman hannuwan ka, balle har ka ringa k'ok'arin had'a kazamin bakin ka mai wari da nawa, ina k'ara gaya maka ka kiyaye ni kayi harkar gaban ka kadai na shiga sabgata kaji nagaya maka."
K'wafa yayi ya fice yabar mata d'akin dan karta bata masa lokaci abokan sa najiran sa a waje.
Yana fita taja wani wawan tsaki tana fad'in "k'aramin d'an iska!".

**********

Fada ta cika makil, hakimai da dogarai sai fad'uwa sukeyi suna kawo gaisuwar su gun mai martaba, wannan yazo ya fad'i ya kawo tashi gaisuwar sannan ya mik'e ya tafi sai wani ma yazo, shikuwa zagi na fad'in "gyara kintsi da kyau".
Bayan ya fad'i sunan ka da kujerar ka.

A na cikin haka sai ga Yarima da tarin abokan sa duk sun sha manya kaya, Yaron Malan ne a gaba sai Yarima a gefen sa, nan fadawa suka shiga yimasa kirari, nan ya fad'i a gaban mai martaba ya kwashi gaisuwar sa.
Haka sauran abokan sa ma suka kawo tasu gaisuwar.

Bayan kowa yagama kawo tasa gaisuwar ne mai martaba yayi ma yarima nasiha mai ratsa jiki, daga k'arshe Yarima da abokan sa suka shiga cikin gida dan gaida iyayan su mata.
Kai tsaye sashin uwargidan mai martaba yayi nan ya tadda wajan cike da jama'a kasancewar yan biki basu gama watsewa ba, ga kuyangi nan birjik ta ko ina suna ganin sa suka hau yimasa kirari da kuran ta shi, nan kansa ya kara girma, nan ya gaida ta suma abokan nasa suka gaidata.
Nasiha sosai itama tai masa nan ya bari shiyyar jikin sa a sanyaye.

